# Yin addu'o'i da karfi Don Batattu

"... su ne marasa bada gaskiya, wadanda sarkin zamanin nan ya makantar da hankalinsu, don kada hasken bisharar daukakar almasihu shi dake surar Allah, ya haskaka su.

An buga sama da Millyan 1

Marubucin
Littafin
Lee E. Thomas.

# BABI 1

# FAHINTAR ABIN DA KE WAJIBI

Batattu ba **zasu taba kubuta ba** sai ko in ana addu'a domin su. Wannan bayani tana gigitarwa kamar ba gaskiya bace, sai dai mun duba tarinhin da Bebul tana bada shi akan batattu ya'yan iblis (Yahaya 8:44) bisa ga umurnin shaidan (Ayukan Manzanni 26:18) Gidan kakarfan mutum (Markus 3:27) damrarun yan yaki (Ishaya 14:17) wadanda suna makance ga bishara (II Korantiyawa. 4:3-4)

Duka wadannan dalilai ne na raunana zuciya abin sai mun yi addu'a domin batattu idan muna bukata su kasance da begen ceto. Amma bari mu fuskanci makancewa ta ruhaniya. II Korantiyawa 4:3-4 Tace "ko da Bisharanmu a rufe take, ai ga wadanda suke hanyar halaka kadai take a rufe. Sune marasa bada gaskiya wadanda sarkin zamani nan ya makantar da hankalinsu don kada hasken Almasihu shi dake surar Allah ya haskaka su. Wannan natsi yana Magana a fili cewar shaidan ya makantar da hankalin batattun mutane domin kada su fahinci bisharan nan.

Lewis Sperry Chafer ya ce "Makatarwa ko nauyin zuciya wanda aka ambata a II Korintiyawa 4:3-4 shine sanadin rashin fahimtar hanyan ceto, kuma baya iya yiwuwa akokarin mutum wanda ya zama makiyin Allah, ya hana Allah aikin ceto halittansa. Wannan batun wata yanayi ne wanda mutum **ba shi da iko** akan sa". (Chafer 57)

Wani Mashahurin mai wa’azi na da Charles H. Spurgeon. Idan ka saurari tattaunawarsa na bada shaida akansa. “Na hurta cewar na zama mai koyar da tsoron Allah ina kudurta in hada hannu cikin addu’a ina kuma wakoki cewar in kwata da Yesu. Na sha jin bishara, duk da haka idan kalmar Ubangiji ya zo wurina da iko yakan zama sabo kamar ban taba ji ba sai ya zama kamar yau ne an saftace ni da jinin mai ceto.

Ya zama kamar na farko ne nake karban bishara kuma rai  ya samu ceto. Na yi tunani kamar ban taba jin wannan ba. Na ci gaba da tunani akan mutumin da na ji wa’azi a wurinsa kamar tun da yake wa’azi bai taba yin wannan wa’azin ba. Amma cikin binbinina sai na gane na sha jin wannan daruruwan wa’azi kamar haka. Wannan akwai bambanci na kanji kamar ban ji ba. Idan na ji ma bai da wani tabbaci a wurina sai na gane yadda na saba jine sai dai ikon ruhu mai tsarki ya bishe ni ya bude kunuwana har na fahimci wannan sakon a zuciya ta.

**Sai na** yi tunani ban taba jin wani mai wa’azi na gaskiya haka ba. Sai na gane an shawo kaina domin haske ta ci gaba da bayanuwa a idanuna, dama ina a makance nike sai na tuna haske bai taba zuwa nan haka ba. Dama haske ya saba haskakawa, amma babu ikon karba.
Tunanin jiki baya hangan ayukan ruhaniya ba” (Spurgeon 26-28)

Misalai na Spurgeon’s yana da karfin shaida bishara ga wanda yake a makance ga hasken Kristi. Idan ana shaida bishara ga wadanda ba wanda yana masu addu’a ba, ya zama kamar mutum ya kama hanun makaho yana ce masa ka duba yadda rana ta fito daga gabas mai kyau zai zama bata lokaci ne kawai domin makaho ba zai gani abinda kana nuna masa ba.

Sai dai ko in Ruhu mai tsarki ya cire makantan Iblis, ya kuma bude hankalinsa da zuciyarsa kafin ya gane bisharan in ba haka ba ba zai taba sira ba domin al’amuran Allah “Wauta ne a gareshi” (I Korintiyawa 2:14)

Kalman wauta a helinanci shine “moria” daga ciki ne aka samo asalin kalmar moro wanda kamus na Webster ta bayana moron kamar wata sani ne mai zurfi wanda mutum yayi binciken sa kuma yana da iliminsa kuma wannan abin ba zai taimake shi ba. Saboda da haka batace yana ganin bishara kamar moronic ne kuma wani banzan abu ne kawai, amma mutuntakan da ke tattare da shi ke kawo masa wandannan tunani mai karfi na wauta akan bishara.

Idan kana kokarin shaida wa wani bishara cikin wannan hali wanda bai hada da wanda ke addu’a dominsa ba irin wannan na kawo barna fiye da gyaranda zai yi. Jessie ya ambaci Penn-Lewis yace sai mun gane mutumin da yana shirye domin fuskantar kalubalai na ikon duhu da makantansa, tunaninsa, da batancinsa akan bishara, in ba kokarine muka yi ba, ba zamu iya fitar da mutane daga ikon duhu zuwa hasken Allah ba. Yan’uwa sai mun san yadda zamu dauki shawara a wurin Ubangiji mu karye karfin mutuntakan nan mu lalatar da dabarun magabci, mu canza nufin mutum zuwa ga sanin Allah da shirinsa na salama” (Penn-Lewis 42-3)

Har idan mun fahinci muhimmanci yin addu’a domin batattu rayuka su sami ceto, zamu koya yadda zamu dinga yinsa. A Janairu 1979 wata batu a mujalla wani mai suna Manley Beasley ya rubuta abinda ya zama hakinmu shi ne “Mu yi wa batattu addu’a” wannan shine manufan bayaninsa “yin wa batattu addu’a ana yawan fadinsa amma sai ko ganewansa kadan ne” yana kama da yadda mutum zai yi kokarin bude wani wurin da shi bai san abinda ke ciki ba, kuma ko yaya abinda ke ciki yake idan ya kai wata matsayi zai zama abin takaici har mu bari.

Amma dawammamiyan rayuka wanda Kristi ya mutu domin su, ba abu ne wanda ya zama a bari ta lalace ba. Saboda haka mu koyi yadda zamu rika yin masu addu’a. A gaskiya watakila ta wurin addu’anka ne za’a ceci

wani daga jahannama. Sanannen mai falkaswa wanda ana ca da shi Charles G. Finney yace “cikin halin darajan abokantaka bai kamata a bar aboki ya lalace ba, ya kamata ya samu ceto daga hallaka. Watakila naka zarafin ke nan wani ya samu kubutaswa” (Finney 54)

Yesu yayi abinda ya gani uban yana yi kadai (Yahaya 5:19) mu ma ya kamata mu yi abinda mun gani ubangiji yana yi ne kadai, abinda yake yi shine “yana ta addu’a” (Ibraniyawa 7:25) mukan yi babban kuskure wajen yin addu’a bai daya akan wasu Krista. Wannan ya nuna wasunmu muna dauke da haki –**BA-HAKABA!!!** Dukan mu ya kama mu yi abinda mun gani ubangijinmu yana yi ne-Addu’a domin wasu.

Saboda haka bari mu koyi yin addu’a dakarfi domin batattu mu goyi bayan ubangiji. mu yi muhimmin abu.

# BABI 2

## TUSHEN BEBUL

Wata dalilin daya zama da karfi domin yin addu'a ya kunshi kawo muhimman dalilai a gaban Allah wadda zai iza shi ya amsa mana addu'o'in mu ya bamu umurni cikin Ishaya 41:21 ku gabatar da masalolinku in ji ubangiji ku kawo **dalilanku masu karfi**..."

Dalilai masun karfi tushen su tana cikin Bebul ne kuma akwai wadannan dalilan da yawa, wadda ya kunshi yin wa batattu addu'a. na yarda da hanyan da F.J Huegel ya bayana, "idan mun samu hanya sai mu kai masalolin masu karfi ga Allah don samun taimako na shaida bishara don ci gaban mulkin Kristi, sai mu fara addu'a da kwazo kamar Bulus ko George Muller ko addu'an Hyde **ya kamata** mu zama da karfi, manyan al'mura zasu wakana (Huegel 80).

Wata babban dalili addua'armu shine muna kaunarsu, an bayana addu'a "cewa" kaunan da guiwa banda haka da ma kaunar Allah ne zuwa ga mutum shi ya kai Kristi kan Giciye: kuma wannan kaunan ne ya sa mai arziki nan ya tuna da Yan'uwansa biyar sa'anda yana cikin jahannama yace ayi masun gargadi don Kada suma su zo inda shi yake (Luka 16:27-28).

Kuma kauna ne tana samu zuwa matsayin yin addu'a domin marasa bangaskiya.

Tarihin Mishan na Pacific Garden a Chicago anyi anfani da shi sosai ta wurin ceton mutane masun yawa kuma an yi anfani da koyaswa jahannama. Bai zama mani da mamaki ba don kimanin rayuka sha-takwas suka nuna alaman rashin yardan su. PACIFIC GARDEN MISHAN" hade da sauran **ADDU'AR UWAYE** wanda ta **BI BAYANSU**. Dawammamiyan rayuwa ne kadai zai nuna yawan rayukan da sun samu ceto ta wurin addu'a da

hawayen da kaunatattu uwwaye suka yi. Da gaske kauna ta zama wata babban kadara ne wajen ceto rayuka.

Bangaskiya wata tushe ne wanda ke cikin Bebul na yin wa batattu addu'a Yesu yace masa dukkan abu mai yiwuwa ne ga mai bada gaskiya" (Markus 9:23) Dukan abu hade da ceton rayuka. Idan zaka bada gaskiya cewar Allah zai ceci wani zai kasance haka. Mutane hudu wanda sun kawo wa Yesu abokin  su shanyaye daya ga bangaskiyarsu sai yace an gafarta maka zunubanka, (Markus 2:5) ko da shike sun kawo shi domin ya samu warkaswa ne, amma ya kai har ma ya samu gafaran zunuban sa. Wannan ya zama babban aikin ban ai'ajibi ne na bangaskiya. Bangaskiya ya zama tsaba ne na al'janna.

Wani abinda na kan ji dadinsa shine yin wa batattu addu'a, kuma Bebul ya bayana irin ikon da addu'a take da shi.

Addu'a mai karfi na adili yana aiki mai yawa inji Yakub 5:16. ba zamu taba gane ikon da addu'a yana da shi ba sai wasu abubuwa zahiri wanda muka jera su sun fara faruwa kafin mu yi la'akari da ikon addu'a.

Aikin addu'a yana kakarye ikonki fiye da tunanin mutum. Idan Krista yayi addu'a iyawansa da manufansa na aika ta abubuwa masun kyau yakan karu fiye da yadda ake zato, kuma ikokin mugaye yakan fadi wannan ba fada'da Magana bane amma dalili shine aikin Allah ne yakan faru don ikon addu'a" (Huegel 10).

A zamanin da aka jefa atomic boam a Jpan a lokacin yaki na II kimanin mutane 92,000 sun mutu. Amma zamanin da Assiriya sun kewaye Urushalima da yaki ya zama sanadin da Hezekiah sarkin yayi kuka ga Allah a madadin mutanensa sai Allah ya aika da male'ika da dare sai male'ika ya kashe sojojin Assiriya 185,000 a dare daya, addu'an Hezekiya ya zama

kamar wannan atomic boam. Idan addu’a tana da karfi hallaka sojoji belle ceton rayuka!

Idan bamu da ginshiki na yin addu’a a cikin Bebul domin batattu, ai wannan ma ya ishemu mu dogara gareshi; Allah yana so mu mika kai ya isa. Allah bai ji dadi ba da yake bai ga wani ya mika kansa domin addu’a kan Israila ba (Ishaya 59:16) wannan ya nuna mani ya kamata ya samu wani.

Ku saurari shar’hi na Andrew akan yadda Allah yana bukatan wani yana roko don wasu: “ ya sha fadi yana jin mammaki a rasa mai roko don wasu kuma ba wanda yana nadama akan mutane har ya dauke nawayan suba. har yanzu akwanakin mu yana dubawa ko za’a samu wasu masun mika kai, domin wannan gaggarumin aiki mai tsarki, kuma wasu wadanda suna yin haka ma basu bada kai cikake. Suna da marmari  amma basu iya jimrewa. Yana jira ko zai samo ma’aikatan bisharan da zasu yi haka, amma suna cewar aikin su ya dame su,basu da lokaci. Kowa yana tunanin aikinsa na farko, ko matsayi, ko jin dadi kowa yana tunani aikinsa kawai. (Murray 144).

Allah ya riga yasa yin wa wasu addu’a ya zama da fifiko a rayuwansu. Mu ji kiranda Allah ke yi, ‘ina gargadi cewa a yi ta rokon Allah ana addu’a ana godo ana gode wa Allah saboda dukkan mutane. Wanda ke son dukkan mutane su sami ceto su kuma kai ga sanin gaskiya (I Timoti 2:1-4).

Kalmar Farko da Helenanci shine:- “Proton” yana bayana cikin Kamus Farkon fari ko na lokaci, ko wuri muhimmin tun da nufin Allah ne mutane su kai ga tsera kuma babu mutum wanda zai tsera ba tare da addu’a ba shi ya saya kamata mu lura da abinda Allah yana so mu yi.

Banda haka wasu muhimman abubuwa masun karfi wanda zamu yi addu’a don batattu sun hada misalinda ke cikin Bebul. Babban misalin duka shine ubangijin Yesu da kansa. Annabcin da ke cikin Ishaya 53. yace Kristi

yana roko saboda lefofinmu” wannan annabci ta cika lokacin da yana kan giciye yayi wannana addu’a uba ka gafarce su domin basu san abinda suke yi ba (Luka 23:34)

Ya kamata Yesu ya zama misalinmu na yin addu’a domin wasu. Saboda har yanzu yana kan yin roko shi ubangijin mu ne da mai cetonmu. Sarkin sarakuna duk da haka yana addu’a yau da gobe baya bari ba. (Ibraniyawa 7:25) Wannan ya tabi zuciya ta don yace saboda yana da ikon ceton masu kusatowa ga Allah ta wurinsa matukar ceto, tun da yake kullum a raye yake saboda yayi masu addu’a.

Bulus manzo shima wani misali ne mai kyau wanda zamu bi. Yace zuciyata na marmarin yin wa Isara’ila addu’a ga Allah domin su sami ceto (Romawa 10:1). An haife mu domin gwagwarmaya ne R. Arthur Mathew ya bayana addu’a shine karshen binciken iko. Idan mutum zai saya sakani ya yi ta godo a memakon mutane wadanda zunubansu zai hallakar da su saboda taurin zuciyarsu sun ki umurnin Allah a rayuwansu (Mathew) Tambayanda za’a yi mana guda daya shine zamu bi misalinsu.

Koda shike akwai wasu tushen koyaswa wanda ke cikin Bebul wanda zamu iya misali da shi saboda irin wannan addu’a ta roko domin wasu. Ina so in ambata guda daya kuma Allah ya riga ya sanya wannan ya zama hakinmu ne.

A matsayinmu na “tsarkakun kungiyan Firistoci” (I Bitrus 2:5) An danka mana hakin wasu domin Firistoci suna wakiltan duniya zuwa samaniya. Hakin mu shine mu tsaya tsakanin mutane da Allah, mu dauki nawayarsu zuwa ga mahalicci. Wannan yayi daidai da abinda Haruna yayi lokacin da ya bada umurni domin ya tsaya sakanin masun raida matattu wanda yayan Isra’ilawa sun zama sanadin ta wurin aikata zunubinsu (Littafi kidaya 16)

Da shike mun damu su samu ceto muna da hakin roko domin batattu. Idan bamu yi haka ba zasu hallaka. Bari mu yarda ruhun Allah yayi anfani damu. S.D Gordon yace ba zai yi jayayya da umurnin Allah a zuciyarsa ba. Wani abin da ban yarda sosai ba shine in fadi abinda ni ban martaba ba domin abinda ni nake gani ba shine wani yana tunani ba. Amma ba zan yi jayayya da abinda mutane sun yarda da shi ba, su wanene wadannan batattun da ake Magana cewar wadandan sun yarda su yi roko ga Allah domin su"

(Gordon 194-95)

Addu'a na shine zaka yarda manufan Bebul mai karfi nan ya fadakar da kai domin yin wa batattu addu'a fiye da yadda ka saba.

## BABI 3

## KEBABBUN SHARUD'DA

Akwai sharudda ko abubuwa guda biyu da ke a kowane amshin addu'a, adalci da bangaskiya. Halin adalci na Krista wanda ta zo ta wurin zub da jini. Shiya sa za mu iya zuwa wurin kursiyin alherinsa gabagadi. Ta zama wajib ne ga addu'a mai amfani. Amma kebabben adalci ma tana da amfani sosai Zabura 66:18 tace "da ban watsar da zunubaina ba da da ubangiji bai ji ni ba" watakila Yesu ya hada duka sa'anda ya ce "idan kuna zaune cikina, zantattukana kuma suna zaune a cikinku, sai ku roki ko menene da kuke so za'a yi maku shi" (Yohanna 15:7) A wata hanya, Krista masu biyayya, addu'o'insu kan samu amsuwa.!!

Wata sharadi mai amfani a duka amsar addu'a shine bangaskiya. Wannan doka ne wanda bata kuryuwa a cikin ruhaniya. A kowane lokaci "Ta wurin bangaskiyarka zata kasance maka" (Matta 9:29). Rashin bangaskiya ta ci gaba da zama mana harin zunubi wanda ta fi dalilin **rashin amshin addu'a.**

A duk lokacin da kuna yi wa batattu addu'a ana bukatan adalci (Hali da kebewa) da bangaskiya. Amma akwai sharudda guda takwas wanda suna da muhimmanci ga wannan hidima. Na farko cikin wadannan shine karaya. "Waddanda sunyi shuki da hawaye zasu girba da farin ciki" wannan shine dokan girbi ta ruhaniya. Duk da haka, muna bukatan girbin amma banda karayar zuciya. Leonard Ravenhill ya taba cewa "Allah baya amsa addu'o'I da yawa wanda suna cike da tausayi ko kuma son kai. Allah yakan amsa addu'o'in da an nace (Ravenhill 110) sai mun nemi rayuka da nacewa kafin addu'armu ta zama karbabbe. Kamar yadda Yesu ya zubar da hawaye a

Urushalima, haka ya kamata muma mu zubar da hawaye akan abokan mu da sun zama batattu, idan muna so su kai ga ceto.

A wani karo ma'aikatan Salvatio Army sun rubuta yanayin da suka shirya domin ribato rayuka zuwa ga samun ceto, da kuma sun fadi yadda ya kamata ayi. Yayi anfani da kalmomi biyu yin amfani da hawaye. Hawaye yana da muhimmanci wajen shaida bishara. Allah ya bada tabacin girbin hatsin (Zabura 126:5-6)

Wata mihimmin sharadi itace wahala wannan hoto tana nuna yanayin wuyan da aka fuskanta lokacin haifuwar yaro kamar yadda mun duba cikin (Ishaya 66:8) sa'anda sihiyona tana gwawarmayan “Samun yaranta”

Ainihin kamus ya bayana wuya kamar wahala cikin zafi mai yawa. Luka 22 yana magana akan Yesu ya dandana wahala wanda har zufa yana diga akoshinsa kamar gudan jinni. Yawancin mu anan bamu taba dandana rayuwa ta samun biyan bukatan amsan addu'o'in mu na ribato rayuka zuwa ga Kristi ba.

Yesu ya bayana dandanawar ceto kamar maya haifuwa” yana daidai da matan da tana dandana zafi wajen haifan jaririnta kuma ya yi daidai da zancen ruhaniya. Bulus ya yi Magana cewa girma ta ruhaniya yana tafiya daidai da jiki. Ya kwatanta da Galatiyawa wanda shi ya ribato su zuwa ga Kristi. Amma kamar yadda na miji ba zai gane tsananin zafin nakudan haihuwan da matansa tana ji ba domin shi baya haihuwa. Wasu Krista basu fahinci muhimmin zafin ribataswa masun zunubi ba. Kimanin matsakaicin Krista casa'in da biyar wanda sun zama tsayayu basu taba ribato rai ko guda daya batun da suke a rayuwansu.

John yana daya daga cikin mashahuran masu “yin addu'o'I”  wani Mishinari mai suna Hyde wanda aka aike shi a India, mutum ne wanda ya bada ransa gaba daya domin addu'oi saboda a samu ceton rayuka. A

**shekara ta 1908** yayi addu'a ga Allah domin ya ceci rai daya kowace rana. A wancan shekara ya ribato rayuka fiye da dari hudu zuwa ga Kristi. A shekara ta biye kuma sai yayi cewa Allah ya tanada masa rayuka biyu kowace rana kuma ba wai ribatowa kawai ba har yayi masu baftisma ya kuma tsarkake su zuwa ga nufin Kristi. Kuma ya ribato sama da dari takwas zuwa ga Kristi. Sai a 1910 yayi addu'a ya samo rayuka hudu kowace rana kuma Allah ya saurari kukansa. Amma a wannan shekara bai ji dadin jikinsa ba ya zama masa dole ya ga likita. Domin mu gane babban wahalanda ke cikin ribato rai, bari mu saurari abinda likita ya fada masa. Zuciya tana a yanayin firgici, an kawas da shi daga matsayinsa na hagu zuwa sashen sa na dama. Ta wurin nauyi da damuwa yana cikin mumunan yanayi wanda ya kai wata da watani ana tsanantawa zai kawo matsayin zuwa zaman lumana kuma. Me ka saba yi da rayuwanka? Sai fa in ka canza daga rayuwan na tsoho zuwa matsayin mika kai na akalla wata shida kana samun wata masala don gina aikin Kristi (Carre 44)

Akwai sakamakon da zamu fuskanta idan zamu mika kai ga ubangiji domin aikin ceton rayuka daga mulkin duhu, amma zamu darajanta su! Bari mu hada hanu domin nuna wannan kauna, kada rayuka su salwanta cikin mutuwa. (Ruya ta Yahanna 14:17) kuma nasara zai zama namu.

Ta wurin wasu kalmomin da sun zama zahiri cikin Bebul yana nuna hoton da ya kunshi hasken batattu. Zamu iya ganin yadda bukatan addu'a akan batattu ya zama dole. Ishaya 14:17 ya bayana batattu kamar wadanda suna daure a kurkuku kuma shaidan ya ki ya sake su.

Ayukan Manzani 26:18 ya fadi mana cewar suna kalkashin umurnin shaidan ne. wata kila yawancin bayanin da Yesu yayi duka a cikin Markus 3:27 akan wani magidanci mai karfi. Ya fadi mana cewa ba wanda zai iya shiga sai dai an daure wannan mai karfin.

Wasu aljanu masu iko haka suke da karfi sai dai addu'a da azumi kadai zai sa mu yi nasara (Markus 9:2a). addu'a da naciya ya zama wajib ne domin in mun bari shaidan zai yi nasara, ba wai Allah ya yashe su bane zai cece su.

Shaidan na iya mulkin kasa da al'adunsu shi ya sa ya zama wa Mishinarai da wahala su kai wa wasu kabilu bishara. Sai bayan shekara bakwai kafin Carey yayi wa mutum na fari da ya tuba Baftisma a India. Sai daya kai shekara bakwai kafin Dudson ya ribato almajiri na farko a Burmali, Marrison kafin ya kawo mai kujera ga Kristi bai samu da sauki ba. Moffat ya fadi cewa yana bukatan bayan shekara bakwai ya ga wata allama ruhu mai tsarki yana anfani da mutanen Bechuana na Afirka. Henry Richard ya rubuta zaman sa na shekara bakwai a Congo kafin mutum na farko ya karbi Kristi a garin Benza Mantaka (Gordon 139-40)

Wani babban makamin da shaidan yana amfani da shi domin ya rinjayemu shine sai ya mai da abubuwa su zama da wahala sai mu bar yin addu'a. dalilin da ya sa yakan yi haka shine bashi da wata makariya na addu'a wata tsohon Karin Magana na cewar shaidan yana ruri duk wanda ya samu sai ya lakwame. Dukan addu'a yaki ne in kuma kayi addu'a, za a rinjayi magabci ko da shike bamu ganin wata sauyawa a yanayin yau da kullum ba. Duk da haka idan mun ga abinda ke faruwa ga ruhaniya in mun yi addu'a za mu samu baban karfaffawa. Mu tuna yadda Allah ya buda idanun bawan Iliya domin ya ga dawakai da karusai na wuta wanda suka tsare su daga abokan gaba (II Sarakuna 6:17) Saboda haka mu ci gaba da yin addu'a don batattu ko mun samu amsa ko babu saboda addu'armu tana samun amsuwa.

Yawancin wadannan yardan da akan dogara akansu ana samu kamar su George Muller. Saboda **yana da nasara sosai a hidimarsa**, cikin

dubawa wandanda ya fara masu addu'a sun tuba, sai yana marmari wannan ne zai zama hanya kadai. Amma a saurari shaidansa game da wannan. Idan nace lokacin cikan shekaru hamsin da hudu da wata tara wanda ina zaman mai bada gaskiya ga ubangiji Yesu Kristi na taba jin an amsa bukatun addu'o'i dubu talatin ko a rana daya ko a sa'a daya wanda aka kawo bukatun. Ba ma zan kai ku da nisa ba. Amma da a ce dukan addu'oin na samu amsoshin duka fa, ka gani haka ba zai yiwu ba, don akwai wani addu'a sai ka jira mako daya ko kuwa wata daya wasu ma har shekara daya ko ya fi haka...A watan Nuwamba 1844 na fara addu'a domin mutane biyar su tuba ina ta addu'a babu kakkautawa, ina ciki haka bayan wata goma-sha-takwas sai na fari a ciki su ya tuba sai na gode wa Allah. Sai na ci gaba da addu'a domin sauran. Sai da na kai shekara biyar kafin na biyu ya tuba. Na nuna wa Allah godiya. Na ci gaba da addu'a domin sauran uku sai da na kai shekara shida kafin na uku ya tuba sauran biyu, sai na ci gaba da addu'a sai guda biyu din basu iya tuba ba. Da shike Allah mai alheri ne ga mutum yana bada dubban amsoshi masu yawa wanda mu muke mika masa don muna addu'oi kowace rana. Na dauki kusan shekaru talatin-da-shida ina addu'a don mutum biyu amma basu tuba ba (Steer 246-47)

Amma wannan ba shine karshen labarin ba. Ya ci gaba da addu'a a kowace rana, kowace shekara sa'anan yace "Babban manufan shine kada ka sadakar sai amsa ta zo. Na yi ta addu'a har tsawun shekara sittin-da-uku da watanni takwas don mutum daya ya tuba. Bai sami ceto ba tukuna amma zai samu. Yaya zai kasance dabam...Ina addu'a". An kai ranan da abokin Muller ya karbi Kristi. Bai faru ba sai ranan da aka sa akwatin Muller a kasa. A wurin, kusa da budadden kabarin ne wannan abokin nasa ya mika zuciyarsa ga Allah. Addu'an naciya ta ci nasara bisa wata gwagwarmaya.

Za'a iya takaita nasaran Muller a kalmomi hudu "Bai yi suwu ba" (Eastman 99-100).

Addu'a yaki ne, ina so in bada shawara cewa addu'a da karfi yana da muhimmanci cikin addu'a domin wasu. Allah ya bamu babba umurni (Matta 16:19) kuma ya zama wajib ne mu yi shi, masamman ma a bishara ta duniya (Matta 28:18-20)

Muna masun nasara ne (Ruya ta Yohana 12:11). Kuma "Mun fi masun nasara nasara" (Romawa 8:37), kuma Allah yana bukata mu "zo wurin" karfafan mutumin nan dake da cikakken kayan yaki mu kuma ci nasara a kansa domin mu "La'latar da kayansa" (Luka 11:21-22). Yadda mun rigaya mun gani, shaidan na rike da rayukan mutane a matsayin bayi kuma ba zai taba yarda ya barsu ba tare da yayi fada ba! Amma mu sani cewa "Kayan yakin mu ba ta jiki ba, amma gaggarumi ne cikin Allah" (II Korintiyawa 10:4) A duk lokacinda muna a shirye domin yaki a tsarin Allah da kuma makamai na Allah mukan yi fada ta wurin addu'a (Afisawa 6:10)

Allah ya riga ya karfafa Ikklisiyarsa da wata gaggarumin aiki da nasara wanda kyamaren hadis ba zasu rinjaye ta ba sai dai kofofin jahannama ta fadada kanta kuma ba abinda zata samu, Ishaya 5:14. na ji tsoro yadda shi Ravenhill ya yi bincikensa.

"Akwai shakewa cikin nuna bambanci a Ikklisiya domin shar'antawa (Ravenhill 80)

Kamar Karin Magana mai cewar karamin sinke ke sokale ido domin an riga an gaskanta da wannan Karin Magana, haka Ikklisiya ta riga ta yarda da rudin shaidan ta wurin rasa ikonta wanda take da shi (Afisawa 1:17-23) kuma bamu anfani da umurni yanzu. Ya ci gaba da kutata kaunar mu har muna nuna bambanci tsakaninmu da wadanda ba Krista ba.

Idan ya zama zamu yi addu'a don wasu, roko yana da kyau. Akwai wadanda sun zama misali a cikin Bebul dayawa, Ibrahim yayi domin Sodom (Farawa 18) Musa yayi domin Israilawa (Fitowa 32). Hezekiya yayi domin yahudawa (II Sarakuna 19) Sauran haka aka ci gaba, roko yana nuna cewar zaka kawo wa Allah dalilan da ke cikin Bebul manufan da kana so ya amsa maka addu'ar ka. Allah ma yana umurtanmu mu kawo masa bukatunmu masun karfi (Ishaya 41:21)

A.T. Pierson yace ya kamata mu yi mahaura akan masalolin mu da Allah ba domin mu shawo kansa ba amma mu rinjayi kanmu. Yadda muna addu'a gareshi ta wurin kalmominsa da manufansa, ya riga ya daure kansa yadda zai shiga sakani, muna nuna bangaskiyarmu wanda shi ya riga ya bamu yanci na roko zai kuma bamu abinda muka roka, mun sani ba zai yi karya ba, ba zai kuma musunci kansa ba (Pierson 150)

Spurgeon ya **yarda sosai akan ikon roko** yace manufan bangaskiya ne idan tana addu'a sai ta sa roko. Karbaben addu'a ya kamata mu yi shi kullum wanda baya addu'a yakan manta da gardamansa ga Allah, amma wadanda suna addu'a domin samun ci gaba mai yawa. Dalilai da gardamansu mai yawa shine suna mahaura akan tambayoyinsu da suke yi ga ubangiji ya yan'uwa ina so mu koyi wannan yadda zamu yi roko in bamu samu abinda muka roka ba sai mu ci gaba da rokon basa ga alkawari da Allah yayi mana. Amma ya kamata mu kasance da abinda muke nema. Kada mu rika lissafta rokon mu, sai dai mu ci gaba da roko domin ya zama kamar madubi addu'a (Pierson 49-50)

George Muller ya duba kalmomi na farko a Zabura 68:5, Uban marayu kuma yayi anfani da wadannan kalmomi domin yayi roko akan gwamraye. Wadannan kalmominsa ne: "Tare da roko Allah wandannan zai zama mahaura na a gabansa, ina girmama shi ta wurin roko domin marayu a

lokacin bukata. Wanda shi ne Ubansu kuma ya sanya kansa ya zama haka kamar yadda yake shine mai tanada masu, nawa hakin shine in tuna masa bukatun wadannan matalautan yara nan domin ya tanada masu. (Pierson 143)

Na tabbata akwai nasoshi da yawa wanda zai jagorance mu cikin addu'oi na roko domin mutane su samu ceto, amma domin gudun lokaci da wuri ina roko ku yarda mini in ambata wasu abubuwa kima. Da zamu iya yin roko ga Allah domin mutum (Irmiya 1:5, Luka 19:10, II Bitrus 3:9, Ayukan manzani 26:18 da Afisawa 2:5-7).

Mukan **roki** alkawarin Allah don mutum ya cetu (Yahaya 3:16,Yahaya 1:12, Romawa 10:13, Yahaya 6:37) mukan roki ikon Allah don ceto (Ibraniyawa 7:25,Romawa 1:16, I Korintiyawa 2:4-5 da Bitrus 1:3-5) mukan iya roki Allah cikin alkawarinsa domin ya rinjayi mutum halittansa zuwa ga fansa, uban ubangiji. Mukan yi addu'a don samun tagomashi na Allah saboda mutum ya samu ceto, ta wurin kaunarsa da alherinsa, nasuwa tsawon jimrewa, roko na wanda ina jin dadinsa shine wanda ya hada da ayukan al'ajibin da yayi domin ceton wasu. Nineva babban birni cike da mugunta wanda Allah ya riga ya sanya mata alama zai hallaka ta, domin matattaran miyagu ne (wanda misalinta yana kama da mahaukacin da yana zaune a kabarbaru baya iya sanya kaya a jikinsa, ya kange hanyan ba mai bi ta wurin haka ma Nineva ta zama birni cika da miyagun mutane wanda suna tsafe-tsafe bautar gumaka) Haka ma da shawulu yake a Tarsus, kafin ya zama mutum mai karfafa Ikklisiya har mutane sun juyo wurin ubangiji ta dalilinsa. (Ayukan Manzani 9:35)

Wata muhimmin batu kuma shine kwatancin wanda zamu yi domin nuna gurbi shine daukan lokaci domin yin addu'a da karfi saboda batattu shine ya zama manufan mu. Kuma wannan addu'a ya zamana na daukakar

Allah (Yahaya 15:7) amma wasu lokatai manufan mu yakan zama ta fahariya da son zuciya. Wani lokaci iyaye sukan yi addu'a domin ya'yansu wanda sun "bijire" tunanin yakan zama na fahariya.

Na dauki lokaci ina addu'a domin mijin yar'uwana ya tuba amma ban gan wata amsa ba. Amma lokacinda ya kamu da ciwon ajali sai na sauya addu'a ta ya zama na neman nufin Allah sai Allah ya bayana mani cewar dama addu'an da nake yi nason zuciya ne. wanda ina ganin in ya warke yar'uwata zata ci gaba da kwanciyan rai da yake Allah ya san manufa ta bai amsa addu'arba, sai lokacinda na sauya manufa ta kafin Allah ya amsa mani roko na roki nufinsa.

Bayanin Bebul afili yake ku roka zaku samu, amma ba domin ku batas da shi ta wurin sha'awoyinku ba (Yakub 4:3) idan dama ka dauki lokaci kana addu'a domin wani musamman ko daga cikin iyalin ne, ko wani aboki na kusa da kai, kuma baka samu amsa ba, to sai ka bincika manufarka ko (dai-dai ne don daukakar Allah).

Cikin dokar kotu alkali bai yarda da hamayan ba yakan fara da tambayo yin yarda don ya gwada gardama ya gani tukuna saboda ya tabbatar da abinda ake nufi ko haka take. Idan alkali ya yarda sai ya goyi bayan mai gaskiya, wannan batu yana tafiya dai-dai da sashen ruhaniya.

Mukan iya yin roko domin masalan batattu mu muna anfani da ayoyin masun karfi a cikin Bebul amma manufan mu ba kyau sai shaidan ya kai karan mu da wannan dalilin sai Allah ya yarda da dalilan da shaidan ya kawo masa sai roke-rokenmu ta zama banza!! Kuma wanda muna addu'a dominsa zai iya mutuwa ya tafi jahannama in manufan mu bai gamshi Allah ba.

Wata babban alaman roko shine sadukar da kai mun koyi wannan daga wajen manzo Bulus wanda ya zama mai mika kai ga Kristi domin samun ceton wasu mutanensa yahudawa. (Romawa 9:3) Na Musa kuma shi

yayi addu’a da azumi na wasu kwanaki arba’in dare da rana domin zunubin mutanensa (Kubawar Sharia 9:18-19). Na Esta kuma tace in na la’lace na la’lace (Esta 4:16) A lokacin da ina koyas da Karin lokaci a makarantan tauhidi a cikin aji na bisharan mutum da mutum na buga wasu jerin addu’a a kati tare da wasu batutuwa kamar haka zan tafi jahannama memakonka. Abin yi anan shine sai mu rubuta sunayen wadanda zamu shiga jahannama memakonsu, sai muyi addu’a kansa sosai. Bayan na rarraba katin da na rubuta wadannan bukatu sai muka hadu a koyarwa na ranan da ta bi bayan wannan nace kowa ya kawo katinsa, sai wani dalibi na ya mike a tsaye yace mani Mallam na amsa sai yace ban yi sammani na shirya shiga jahannama a madadin wani ba. Sai yayi mana magana sosai. Ko da shike Allah ba zai yarda mu dauki matsayin wasu a jahannama ba amma tabbaci yawan addu’armu zai karu in mun mika kai don yin haka!!

Dukan sauran abubuwa dai-dai, amma hadin kai yana da iko wajen addu’a domin batattu, yakan haifar da amsa mai sauri!! Ya zama kamar wata ma’aikata wanda ta riga ta yi zafi idan an kunna wuta zata amsa kawai ya kamata mu Krista manufanmu ya zama daya domin fuskantar kowane kaubale da ke gabanmu, idan muna addu’a muka sa mutum daya a gaba zamu iya yin nasara da sauri ikon Kristi yana kansa.

Wannan shine abinda ya faru a babban taro (Convention) na yaron William Carey’ Jabez. A lokacinda ake taronsu na shekara na Mishinarin Baptist wanda aka yi a London sai Dr. Ryland ya dau nawayan Jabez yace “Dan’uwa bari mu aika da hadaden hada hanu na addu’a zuwa ga Allah a murya daya da manufa daya sai Jabez Carey ya sauku.” Saboda haka sai Ruhu mai tsarki nan da nan ya sauko wa masun taron kimanin mutane dubu biyu wanda suka dauka ninyan roko don wasu. Sai Carey ya karbi wasika daga wajen Jabez yana gaya masa yadda shi ya samu sauyi da kuma

"**Lokacin da ya samu falkaswa dai-dai da sa'oin da suke roko domin jama'a**" Gordon 87-88.

Jim Cymbala ya fadi yadda shi ya shirya wa yar'uwanshi Chrissy addu'a ya dauki kimanin shekara biyu da rabi amma bai samu wani amsa ba. Sai wata rana ne cikin haduwan su ran talata da dare domin addu'a a wani wuri ana kira Brooklyn Tabernacle sai wata yarinya tace tana ji suyi wa Chrissy addu'a. a wannan ranan ne Ikklisiya ta juya hankalin su gaba daya sun ci gaba da addu'a mai karfi. Ta wurin haka aka samu cikaken canji, kamar ace shaidan ba zaka kara samun yarinyan nan kuma ba ka dauke hanunka akanta zata dawo, nan da nan bayan sa'oi talatin da biyu sai ta yi hakan (Cymbala 63-65).

Lokacinda Pastor na Ikklisiyar New Hope Baptist a Jones Louisiana ya kalubalanci mutanensa su rubuta sunan wani wanda su suna so su gani ya tuba a warkan tagarda su kawo shi ya gani, kuma suna ninyan bada kai su yi addu'a domin wannan mutumin, sai mutane goma sha takwas sun rubuta sunan "Mike Doles" bayan makoni biyu sai ya tuba.

Helen Gresham ta dauki shekaru goma sha takwas tana addu'a domin mai gidanta ya tuba amma bata yi nasara ba, sai ta roki Pastonta Mickey Hudnall ya taimake ta sai su biyu suka dukufa cikin addu'a sai Ricky ya tuba basu kai wata biyu cikin addu'a ba kuma abin farin ciki ne yadda ubangiji ya ba shi aiki wanda yayi masa yanzu, shi kansa bai san matansa da Pasto suna addu'a domin sa ba.

Bari mu dubi irin ikon da addu'o'in mutane suna yi domin batattu. Mutum dubu biyu sun yi addu'a domin Jabez Carey sai ya tuba a wannan, mu duba kuma na Chrissy Cymbala ita ma ta samu mutane dararuwa suna addu'a dominta sai nan da nan ta tuba cikin sa'oi talatin da biyu. Na Mike Doles kuma ya samu ceto cikin mako biyu saboda mutum sha takwas sun yi

masa addu’a. Mutum biyu sunyi addu’a domin Ricky Gresham shi ma ya samu sauyawa watani kusan biyu!!

Hey yace idan ka samu wani yana taya ka addu’a akan dan’uwa ko aboki zaka ga abin ban mamaki!! Cikin yakin ruhaniya mutum biyu zasu kori dubu goma (Kubawan Sharia 32:30) kuma in mutune biyu sun yi “muwafaka cikin addu’a zasu karbi abinda suke roko wurin ubangiji” (Matiyu 18:19).

Bari in fadi maku yadda hadaden addu’a yana da iko domin batattu. Na fari ma shine abinda Allah ya fi martaba a amu hadin kai a wurin mutanensa. Wannan shine abinda ubangiji yana bukata, shaidu ko bukatun mu na addu’a (Yahaya 17) yayi addu’a sau biyar domin mu zama daya kuma abinda ya zama na farko a wurin Allah wanda yana so muyi shine muyi wa mutane addu’a domin su samu tsira (Timoti 2:1-4) Tun da zumunci tana da anfani gwalgwado soboda roko don wasu “Allah bai samu ko guda daya a Isarila ba” (Ishaya 59:15). Idan ka hada wannan a wuri guda, zumunci da roko don wasu ya zama ninki ne. Allah yakan dauka haka nan da daraja sai ya kawo albarka wanda ya fi gaban kwatanci!!!

Manufa na biyu mai sauki ne akwai mutum mai karfi daya wanda yana shugabanci rayuwan mutum. Sai mutanen Allah masun yawa suka fuskanci mai karfi guda dayan nan za’a kada shi da sauki domin wanda yake cikin mu ya fi wanda ke cikin duniya karfi (I Yahaya 4:3-4). Sai kuma “La’latar da kayansa” yana da dangantaka mai sauki. Wasu lokatai wadannan batattu zasu zo wurinku neman taimako. Wannan shine abinda ya faru da Jimbo Barrentine. Na yi alkawari da matansa Rachele a Janairu saboda muyi masa addu’a. Bayan watani biyu sai ya shiga yana neman tuba sai ya zo ofishina nema na. Amma ina Arkansas koyas da wadannan kayayyaki na addu’a cikin babban taronmu sai ya tafi gidan wani mai wa’azi a cikin Ikklisiyanmu domin

nemi hanyan da zai samu ya tuba. Bai iya daure ya jirani in dawo ba, yayi kokari domin ya samu ceto nan da can!

Dalili na uku shine fahariya yana rushewa. Shaidan ya sanya fahariya a zuciyarmu kamar yadda Allah ya sanya yabo a zuciyarmu. Sai fa mutum ya kaskantar da kansa kafin ya roki taimakon addu'a domin magabci zai ci gaba da yaudaran al'amuran. Bayan wannan Allah da kansa yana "tsayayya da fahariya amma yana bada alheri ga wadanda suna kaskantar da kai" (Yakub 4:6) sau da dama idan ina so in shaida bishara ga batattu maza sai matansu su fara bayana mani kyawawan ayukansu. Fahariya baya barinsu su yarda da kasawarsu a gaban Allah. Wahalan shine ban taba samu in rinjayi daya daga cikin wadannan mutane zuwa ga Kristi ba.

# BABI 4

# ROKO TA MUSAMMAN

Yawancinmu yakan zama mamu da wuya mu yi addua'a don wani ya tsira saboda abinda mumun iya shine mu fadi "Allah muna roko ka ceci wane da wane." Mu kan yi maimaici irin ta wofi mu yi ta anfani da kalma guda in mun gaji sai mu sadukar. Abin nufi anan shine irin wannan addu'a ya kumshi abubuwa hudu, anihin mutumin kansa, ran da – za'a ceta, Maganar Allah, da kuma fadakarwa. Idan mun koyi addu'a rokon mu zai kasance kalubale da kuma anfani.

Ga yadda za'a fara muna addu'a domin wane, sunan sa ka nemi ubangiji yayi abubuwa biyar a rayuwan sa. Na farko mu roki Allah ya tsarkake shi. Watakila wannan zai zama maka kamar bakon abu amma haka Allah ya fara aikin ceton sa, a rayuwan ko wane mutum. Ya kan fara tsarkake mutum ko kwa ya "Kebe" mutumin domin cetonsa kafin ya cece mutumin.

Bebul ta nuna wannan koyaswan Zahiri gaskiyan cikin I Bitrus 1:2 "Su da ke zababbu bisa ga rigya sanin Allah uba, wadanda Ruhu kuma ya tsarkeke, domin su yi wa Yesu Almasihu biyayya, su kuma sarkaka da jininsa" Mun gani an na'nata Magana dayan ne II Tasalonikawa 2:13-14 ya ku yan'uwa kaunatattu ubangiji lalle ne mu gode wa Allah saboda ku, domin Allah ya zabeku ku fara samu ceto ta wurin tsarkakewar ruhu, da kuma amincewar ku da gaskiya.

Yana daidai kamar yadda Allah yakan fara kewaye mutum da ke wurin kafin ya fara albarkantan sa. Yana da sauki a gani abinda yake fito daga "ciki" shi yake tsarkake mutum da sauri har ya shafi rayuwansa wanda yake cikin Kristi. Idan Allah kansa ya kasance cikin wannan kewayan shine yakan

sa a martaba shi sai manyan al'amura su fara wakana, kamar yadda in ka karanta wata littafi mai suna personal testimonies later.

Wannan tabbataciyar al'amura yana karfafa mu wasu da muke addu'a don sauran mukan tabbatar cewar Ruhu mai tsarki daya zama ubangiji girbi yakan ceci mutum wanda shi ya kebe. Wani dalibi na koleji wanda yana makaranta ta taba rubuta wa C.S. Lewis yana bayana mashi yadda ya sadu da wasu dalibai Krista wansu na shaida masa Maganar Allah da kuma yadda su sun tsaya akan bangaskiya su. Wasu abubuwan da daliban nan sun gaya masu ya ci gaba da damunsa a ransa yayi ta gwagwarmaya da shi a rayuwansa. Sai ya ce Dr. Lewis menene kake sammani? Sai Lewis ya rubuta ya meyar masa cewa "kana tsakiyar raga Ruhu mai tsarki yana tare da kai. Ina sammani ba zaka kubuta ba" (Dunn 118)

Yanzu mun roki ubangiji ya albarkace shi. Lokacinda Yesu ya aiki al'majiransa zuwa "girbinsa" ya basu umurni na musamman na "farko ku ce salama ta kasance a wannan gida" (Luka 10:1-5). Tunda shike Alherin Allah ne kullum ya jagoranci mutane zuwa ga tuba (Romawa 2:4). Wajib ne mu kawo rokon mu ga Allah ya albarkace su domin alherine muyi haka.

Amma wata lokaci idan mun yi addu'a saboda samun cetonsu sai bamu samu amsan addu'ar mu ba sai muji takaici mu kasa hakuri a zuciyarmu. Sai mu fara tunani da Allah ya "Koya masu hankali wata masala". Lokacinda wannan kauye ta samariyawa sun ki ubangiji sai al'majiransa sun so da Allah ya saukar da wuta a wannan wurin domin ya kone mutanen nan take. Ya kwabe su da cewar "Ku baku san wane irin ruhu ne yana tare da ku ba. Saboda dan mutum baya zo ya hallaka rayukan mutane bane amma domin ya cece su" (Luka 9:52-56) idan zamu koyi halin mai ceto ne zamu ci gaba da marmarin Allah ya cece mutane. Ya kamata mu yi masa roko na musamma domin samun albarkansa ga wadanda muna addu'a saboda su.

Na uku mu roki ubangiji ya nuna masu su yarda da zunubinsu. Su kuma tabbatar suna bukatan ceto. Ruhu mai tsarki ne kawai zai tabbata wa mutum cewar shi mai laifi ne. saboda haka mu zama masun kokarin roko Yahaya 16:8-11 cikin addu'armu. Ganewar kuskure na nufin mutum ya yarda da kasawarsa. Domin damuwar batattu nan yana kansu ne sukan "kasa bada gaskiya ga Yesu" kuma wannan shine ZUNUBI wanda ya zama na saba wa ruhu ke nan (Yahaya 16:9).

Mutane sun riga sun sani suna "Zububi" sai dai zunubi na marasa bada gaskiya cikin Kristi. Tunda wannan shine zunubi wanda yakan kai mutum jahannama, shaidan ya makatar da tunaninsa a wannan wurin. Saboda haka Ruhu mai tsarki yakan nuna ko ya sanashe su, wannan shine hanya kadai wanda akan bayana masu cewar ubangiji Yesu Kristi ne mai daukaka ta wurinsa kadai zasu samu ceto. Ya kamata mu sani cewar idan an nuna wa mutum kasawarsa har ya yarda ba wai ya zama tabbacin ceto bane, kamar yadda Bulus ya bada bayani akan adalci kamun kai da hukunci yana zuwa Filibus ya kadu har ya kada kai (Ayukan Manzani 24:25) Amma babu wani tabacin bayani daga Bebul wanda ya nuna cetonsa.

Na biye shine mu roki Allah ya dawo da hankalinsa saboda ya san gaskiya ko da shike in wani ya zo ta wurin cewa yasamu tabbaci cewar an nuna masa bukatansa na ceto amma zuciyarsa a makance yake akan ceto zai ci gaba da zama makaho tunda bai iya ganin hasken bishara na Kristi ba kuma zai ci gaba da zama a ikon duhu (II Korintiyawa 4:6) Amma idan har zuciya ya bude ga sanin gaskiya sai Allah yayi anfani da Krista domin su bayana masa wannan bisharan. Ko da shi wannan Baba na Itobiya yana bidan gaskiya ne ya zo Urushalima musamman domin yayi sujada ne kuma sai ya samu wannan ayan yana karantawa, amma bai gane ba sai ko in wani yayi masa bayani Ayukan Manzani 8:26-39.

An ci gaba da bayana labarin ne har zuwa na Karlinus (Ayukan Manzani 10) Dama shi mai ibada ne kuma “Yana zaman tsarki mutum ne mai tsoron Allah da dukan gidansa duka wanda yana bada sadaka kuma yana addu’a ga Allah kullum” kuma zamansa ya yi kyau fiye da wasu Kristan da mun sani amma har yanzu mutum ne mai mutunci amma batacce ne. Bai gane hanyar ceto ba, dama ya samu umurni ne daga wurin mala’ika cewar ya aika wurin Bitrus wanda zai “fada masa abinda ya kamata yayi.” Karlinus da wadanda suna zaune tare suka bude wa bishara kofa nan da nan da suka ji “kalmar” sai ruhu mai tsarki ya sauko masu sai suka samu ceto. Tun Bitrus yana jawabi tukuna!!

Kayi addu’a ka roki Allah ya bude zukatan wadanda sun zama batattu. Zai iya yi har suma su samu tsira.

Yan’uwa muna shirye mu ce wa ubangiji ya cece shi. Muna a shirye mu roki Allah ya nuna dukan ikonsa domin mutane su samu ceto, don Allah yana iya sauye al’amura cikin rayuwa wanda shi ya shirya domin ya kawo mutum ga tuba.

Cikin Luka 19:10 yace dan mutum ya zo neman abinda ya bata don ya cece shi Chafer yace ya fi karfin kokari kawai don ceton abinda ya bata domin wanda yana rike da su mai karfi ne saboda haka yana bidan ikon Allah ya cece su daga hallaka zuwa ceto (Chafer 3-4) iyalin Tony Fontenot’s sun yi addu’a don samun ceton sa, sun dauki lokaci suna addu’a shekara da shekaru, sai sun gani kamar addu’an su ya zama banza, sai ran 22 Mayu na 1982 a wannan rana ne ya samu hasarin jirgin sama sauran kadan ya kone sai Allah ya ja hankalinsa komai ya zama da sauki!

Idan mutum yana so ya karbi bishara, sai wani ya shaida masa. Babban abin yi shine muyi addu’a ga ubangiji domin ya aika da wani domin wannan aiki. Azahirin gaskiya abinda aka aikemu mu yi kenan, “anihin girbi

tana da yawa, amma ma'aikata sun kasa. Ayi addu'a domin ubangijin girbi ya aika da ma'aikata zuwa wurin girbinsa" (Matiyu 9:37-38).

Saboda da ma'aikata kima ne wanda yana nufi cikin bayanin kamus ana nufi zamu yi addu'a domin neman taimakon Allah. Na farko zamu yi addu'a domin ya aika da Karin ma'aikata. A kalman Ibirnanci "ekballo" yana da ma'anan tilastawa watau ana anfani da dole a aika, ko a aiki wani ko wasu, ko a jefa.

A tuna wahalan da Allah ya fuskanta lokacin aikan Yunana zuwa Ninevah domin yayi wa'azin kalman sai da Allah ya dolance shi kafin ya tafi. Wani abu makamanci haka na faruwa idan Ikklisiyar Allah suna manta da aikin bishara sun dauki wasu ayuka fiye da abinda ke gabansu. Allah ya yarda tsanani ta afka wa Ikklisiyar Urushalima sai suka warwasu a dukan yankunan judiya Samariya da sauransu" (Ayukan Manzani 8:1) amma " su da suka warwasu ko'ina suka ci gaba da shaida kalman" (Ayukan Manzani 8:4).

Tun da ma'aikata ba kima bane shi yasa Puny (Kalma) ya bada umurni mu roki Ubangiji ya horas da ma'aikata domin su ingantu saboda su zama da muhimmanci ta wurin shaida kalma. Ya kamata mu gane cewar wadanda aka horas dasu su zo ta wurin ruhu mai tsarki Samuel Chadwick ya ce "Ikon Ruhu yana hura daga gareshi Allah baya barin numfashinsa a banza. Ikon sa baya koma banza, bayanuwarsa baya zama banza,... ba wai yana bada iko kadai ba. Yana kerawa, domin kada wani ya kasa" (Chadwick 89).

Don haka ne Yesu ya umurci almajiransa su jira cikin Urushalima sai an yi "Maku Baftisma da ruhu mai tsarki" (Ayukan Manzani 1:4-5) sai y ace masu "amma zaku sami iko sa'adda ruhu mai tsarki ya sauko maku zaku kuma zama shaiduna a Urushalima da dukan kasar Yahudiya da Samariya har zuwa iyakan duniya" (Ayukan Manzani 1:8)

Ko da shike cikawa da ruhu mai tsarki shine yancin sake haihuwar mu (Ayukan Manzani 2:38-39) Dukan Ikklisiya tana da masaniya kima game da yadda ake “mika mamu ikonsa mu da muka bada gaskiya gareshi” (Afisawa 1:19) Domin rashin kulawarmu dubban rayuka suna fadawa cikin jahannama domin rashin kulawarmu, bamu da ikon da zamu dakatar dasu, in ba tare da taimakon ruhu mai tsarki na Allah ba iyawarmu ya kasa. Saboda haka zamu yi addu’a ga Allah domin ya aiko da ma’aikatansa wanda suna cike da ruhu mai tsarki ana inganta su da iko (Hikima da tilastawa) su kasance da gaba-gadi (Ayukan Manzani 4:31) Hikima (Karin Magana 11:3) Ninya (Kolosiyawa 4:12-13) Tausayi (Yahuda 22-23) Baiwa (Irimiya 33:3) kuma rayuka zasu cetu!!!

Bayan mun yi addu’a domin su samu ceto da kuma ma’aikata su shaida masu, sai kuma mu yi addu’a domin kalmar Allah da za’a shaida masu. Dalilin haka kwa domin babu wanda zai tsira ba tare da jin kalmar Allah ba (Romawa 10:14) Na biyu kuma shaidan baya son kalmar Allah, saboda haka zamu ci gaba babu suwu muna fuskantarsa ta kowace hanya domin mu iya kwace mutane a hanunsa. Tun da maganar Allah ya zama da muhimmanci don nuna wa mutum kasawarsa. (Ayukan Manzani 2:37) don yantaswa (Yahaya 8:32) da kuma ceto (Bitrus 1:23) batattu shaidan yana tsayawa da karfi domin yayi hamaya da hallakaswa (Luka 8:11-15) maka mai (II Korintiyawa 10:4-5) yaudara (II Korintiyawa 11:3-4)

Kamar Allah a wurin shaidan kamar banjo a hancin kakkarfan mutum ne yana sa shi ya zama kumama har ya tsume babu karfin tsare mallakansa sai ya zama dole ya yantar da wadanda shi ya tsare su ta wurin haka mutanen zasu san “gaskiya kuma gaskiya zata yantar da su” (Yahaya 8:32) amma ka sani cewar ba gaskiyar ne ta yantar da kai ba, amma gaskiyar da

ka SANI ne ya kubutar da kai. Saboda haka shaidan yakan yi iyakacin kokarinsa domin rikitar da mutum wajen “sanin” gaskiyan nan.

Cikin bayanin da yayi akan mai shuka wanda yayi wa almajiranci. Yesu yace shaidan ya zo NAN TAKE ya sace maganan a wurin mutumin domin kada ya gane (Markus 4:15) Wannan ne ya sa ya zama wajib mu yi addu’a domin a shaida wa batattu maganar Allah kuma su gane.

Cikin yin addu’a Allah yayi anfani da kalmar sa domin batattu su tuba mukan roka abubuwa biyar ta musamman. Na fari shine maganarsa ta “samu yaduwa” (II Tasaloniyawa 3:1) Ana nufi kada ya samu cikas: watau kada shaidan ya samu dalilin da zai dakatar da maganar Allah watau kada mutane su gane gaskiyan nan su rika shakka akalman ubangiji da rashin tabbas.

Na biye shine muyi addu’a maganar Allah ta samu daukaka (II Tasalonikawa 3:1) wannan na nufi tayi sauri yado ta sami daukaka a tsakiyar wadanda suke saurara. Zamu samu sabon girma ta wurin maganarsa lokacinda sunansa ta “samu daukaka fiye da kowane suna” (Zabura 138:2) Tabbaci Allah shine Kalmansa kuma yana tsira. Tun fil’azal akwai kalma, kalman kuwa tare da Allah yake, kalman nan kuwa Allah ne, kalman nan kuwa ya zama mutum ya zauna cikin mu” (Yahaya 1:1,14)

Muna addu’a kuma maganar Allah ta habaka (Ayukan Manzani 12:24) Daya daga cikin dokokin girbi shine idan mutum ya shuka iri a yalwace zai girba a yawalce (II Korintiyawa 9:6) Mukan yi addu’a kuma domin maganar Allah ta habaka ko ta yadu (Ayukan Manzani 19:20). Haka kamar karamin iri yakan fasa kasa domin karfin ingancinsa, haka maganar Allah idan ya shiga zuciyar mutum zai tilasta shi ya bi nufinsa, saboda yana dai-dai kamar yadda aka shuka iri ne cikin zuciya.

Addu’a wanda nakan ji dadinsa shine wanda zai zama da karfi har mutane su tuba (Ayukan Manzani 14:1) yace suka yi “Magana sai taron jama’a Yahudawa da Helenawa masun bada gaskiya sun zama daya” Mukan roka Ishaya 55:11 “To haka maganar da na fada take, bata kasa cika abinda na shirya mata. Zata yi kowane abinda na aike ta ta yi.” Allah yana so maganarsa ta zama da karfi, ka rike shi ya zama haka kuma zaka rika addu’a cikin baiwansa, da nufinsa kuma za’a amsa addu’arka!!

Bari in tuna maka cewar Yahuda Iskaryoti ya kasance da maganar Allah sosai amma duk da haka ya mutu ya kuma tafi jahannama wanda Yesu yace “gwamma da ba’a haife shi ba” (Markus 14:21). Farisawa wadanda sun zama masun addini akwanakinsu- amma kaitonsu domin suna iza wa mutane kaya mai nauyi su kuma basu aikatawa, suna nesa da aljannan Allah ba zasu samu ba.

Bari mu gane sai dai in ruhu mai tsarki ne ya shuka Magana akunnen mai ji. Kafin mutum ya tsira. Wannana ne dalilin da ya kamata mu yi addu’a domin kalmar Allah ta zama da karfi a kunuwan masu ji!!!

Idan muna bukata mu gani jama’a sun tsira to ya kamata mu zama masun addu’a domin falkaswa. Ayoyin falkaswa sun fara a hanyoyi kamar haka. “Idan mutane na wanda ake kiransu da suna na zasu kaskantar da kansu su yi addu’a su nemi fuska na (II Labarbaru 7:14) irin addu’an da aka bayana anan ta roko ce yin wa wasu addu’a. Sai da bayan Ayuba yayi addu’a (Wasu kalmomin Yahudanci kamar yadda yake a bisa) na abokansa wanda cikin wata yanayi na ban mammaki ya sauya ra’ayinsa (Ayuba 42:10).

A lokatan falkawa akan yi addu’o’i a hada duka da na wasu. Duncan Campbell ya bayana falkaswa kamar mutane sukan “jika sharaf da Allah” (Edwards 26) idan mutane suna ma’amala da Allah sukan damu da wasu

fiye da yadda zasu damu da kansu. Tausayinsa domin rayuka yana sashi ya zubas da hawaye!!

Saurari yadda Finney na bayana rinjayan addu'a lokacin falkawa na fadi fiye da sau daya cewar ruhu addu'a na rinjaya yawancin wadancan rinjayan akwai masun sa alama na nan gaba yana da sauki wadanda suka fara tuba su koyi yin addu'a da kuma wasu misalai don ya basu hanyan nasuwa cikin addu'a na dukan dare, har zuwa matsayin da zasu samu karfi na mika jikunan su saboda ceton rayukan da suke kewaye da su. Dama akwai babban izawa ta ruhu mai tsarki a zukatan Krista kuma ya kamata su masu yi hakuri da wadanda ana ceta domin hakin sune su lura da rayukan da ana same su domin zasu dawama: Yana da sauki a samu Kristan da sukanhadu a wasu wurare suna tade-tade memakon su durkusa a gwuiwansu domin addu'a.

Ba don taron addu'a kawai ba amma zai zama da babban habaka ta wajen halara……… amma dama akwai ruhun addu'a a kadaice. Krista suna addu'a sosai yawancinsu suna daukan sa'o'i suna addu'a a kadaice: kuma ya kunshi mutum biyu ko fiye zasu dau alkawari. "Idan ku biyu zaku yi yarjejeniya akan wani abu anan duniya wanda zaku roka za'a yi maku domin daukakar ubana wanda ke cikin sama, in ma zaku roko akan wani abu, ko mutane zaku samu. Amsan addu'a takan bayana a hanyoyi da yawa, wanda ba wanda ba zai yarda cewar Allah bai amsa ba, akullum da kuma kowane lokaci Allah yana amsa addu'armu (Finney 141-42) kamar yadda ka'ida na karanta falkawa ya sa aka gane cewar falkawa na kawo yadda ake ceton darurukan rayuka, har ma dubbai zuwa Milliyan na mutane wanda suke tsira ta wurin karban Kristi su kuma zama Krista. Jonathan Edwards yayi la'akari cewar falkawa ya zama wata ginshiki ne wanda Allah na anfani da shi domin

fadada Mulkinsa. (Edward 26). Saboda haka idan kana so ka ceci rayuka, sai ka yi addu'a domin falkaswa!!!

# BABI 5

# YAKI TA RUHANIYA

Babban manufan yin addu'a don batattu ba domin mu shawo kan Allah ya cece su ne ba, domin shi "baya son wani halittansa ya hallaka" (II Bitrus 3:9) an aiko Kristi ya mutu saboda zunuban duniya (I Yahaya 2:2) amma yana dauke da yaki ta ruhaniya ana yantar da su a ikon aljannu saboda su sami tsira.

Takaitacen dubawar Bebul a bayaninsa irin ninyanda ake ciki na neman sani zai sa ayi bincike har a gane gaskiyan batun. Batattu suna cikin kurkuku ne wanda shaidan baya so ya sake su (Ishaya 14:17) bayi a kalkashin ikon shaidan (Ayukan Manzani 26:18) Ya'yan Iblis (Yahaya 8:44) suna makance ne ga bishara (II Korintiyawa 4:3-4) suna samun karfi daga wurin shaidan (Afisawa 2:2) Babu cikaken samun taimakon domin daga wurin shaidan ne. Shaidan ya riga ya kamasu (I Yahana 5:19) kuma magidanci mai karfi (Markus 3:27).

Cikin wannana takaitacen bayani zamu gane hoton wasu ayoyi Misalin Afisawa 2:2 yace tunanin abinda ya wuce zai kawo rayuwa irin ta wannan duniya dai-dai da sarauniyan ikon sararin sama ruhun da ke rayuwa cikin ya'ya kangara kalman Helinanci na rayuwa shine Energeo- watau "Karfafa" wannan tana nufi ke nan batattu suna samun karfafawa ta wurin ruhu Iblis. Ba shakka batacen mutum bai san hakannan ba. Lallai ne bai sani ba, da ya sani dab a haka ba. Yana tunani shi ayance yake (Wannan yana daya daga cikin bacewar da yayi) amma a gaskiya abinda yake aikatawa yana zuwa ne daga ikon sarauniyan sama" (Dunn 120)

Bari mu duba (I Yahaya 5:19) "Mun sani muna Allah ne duniya duka kuwa tana hanun mugun" wannan ana nufi dukan duniya (hade da

mazaunan ta) suna kwance gaba daya suna biyayya da mugun. Kamus na Webster ya bayana biyayya shine kwanciya da fuska a kasa watau ayi rub da ciki fuska a kasa: Watau mutum ya mika kai duka. Abinda ake nufi da wannan ayan shine mika kai ga abinda ke na duniya ko mai yana hanun mugun cikin kalkashin mallakansa. Har'ila yau yana kwance a wurin. Ba wai zamansa a wurin yana kokari da ya samu yanci bane, amma yana kwance shiru, watakila cikin kwancen ma ya tsume a hanun shaidan. Mugayen ba su iya taba Krista, amma duniyan nan bata da abin taimako cikin lulluban da ta yi mana. (Stott 193)

Sai kuma Markus 3:27 shine wanda na yi la'akari da shi yana da muhimmanci cikin ayan a Bebul wanda zamu yi anfani da shi domin ribato batattu zuwa ga Kristi. Cikin wannan ayan Yesu da kansa yace. "babu mutum wanda zai shiga gidan mutumin nan mai karfi ya washe kayansa, sai dai in ya fara kama wannan mutumin ya daure shi kafin ya iya washe gidansa wannan ayan tana nufin wani abu, ake nufi shine ba wani batacen da zai sami tsera sai ya sami wani ya yantar da shi daga tasirin ikon aljannu. Wannan shine anihin abinda za'a fara yi da farko. Wannan yantaswan zai samu asalin daga wajen addu'a! kafin mu ci nasara a yakin ceton rayuka wadannan sune wasu abubuwanda ya kamata muyi. Na farko mu yi anfani da makamain da Allah ya umurce mu da shi. Lokacinda kawuna Sam ya kore ni a aikin soja aiki na shine yin anfani da makamai cikin yakin Vietnam. Ya kamata in saba da M-16 dina yadda zan kafa shi in kuma harhada shi ko cikin duhu domin abinda ya kamata in yi kenan cikin dagan yaki.

Allah ya tanada mana makamai masun karfi wanda zamu yi anfani da shi a wannan yakin ruhaniya "domin kuwa **makaman** mu na fama ba na mutuntaka bane na ikon Allah ne, masun rushe makamai masu karfi

(II Korintiyawa 10:4). Damuwarmu shine ko mun saba da makaman mu ko yakin kansa babu ashirye muke.

Amma kafin in dan koyas da ku yadda zaku yi anfani da makamanku, bari in tuna maku cewar anihin kayan shine addu'a muna yaki, a **yawan lokaci duka cikin addu'a** yakin kuwa ta ruhaniya inji dan'uwa Mackey Bonner rashin addu'ar mu kuwa shine nasaran shaidan, amma idan muna **addu'a ba shi da wata kariya**, shi yasa Allah ya ce mu yi ta addu'a babu fasawa" (I Tassalonikawa 5:17) me yasa manzani sun **ci gaba da addu'a** saboda hidima a duniya (Aykan Manzani 6:4)?

Hakanan kamar yadda makamai na zahiri suke haka ma na ruhaniya suke, ko na ruwan boma-bomai, ko na Farmaki, ko na aman wuta, ko na kakkabe makamai, ko mansun linzami da dai sauransu. Wadannan kayan duka mutum yayi su domin cin nasara akan abokin gabansa, haka makamai ta ruhaniya suke, muna yi ne domin mu yi nasara, saboda haka ya kamata mu saba da makaman mu ta ruhaniya wato addu'a.

Wani babban makamin mu shine **jinin Kristi** (Wahayin Yahaya 12:11) yace "Sun kuwa yi nasara da jinin dan ragon" Ibraniyawa 2:4 ya fadi mana ka roka cikin jinin Yesu yana da iko "Ya dauki kamanin haka domin ya hallakar da mai iko mutuwa wato Iblis ta mutuwarsa" kamus mai karfi ya bayana hallaka a "mai da abin babu anfani, ya lalace"

Sa'anda shaidan ya jirgita dan Allah wanda bai yi komai ba ya hallakar da kansa ne, ba wai ya rushe kansa bane, ya hallakar ne. dukan hakinsa a duniya wanda ya nema ya samu a duniya musamman akan faduwar mutum, Adamu yanzu an sauke wannan, tunda shike ba shi da iko da zai hana Gicciyen da Kristi ya dauke yanzu, ya nuna bashi da wani iko yanzu. (Billeimer 31)

Idan muna addu'a cikin suna Kristi muna tuna wa shaidan da dukan aljanu cewar an riga an ci nasara akan su. Wannan nasara ne na musamman akan gwagwarmaya ceton rayuka tun da yayyafawar jinin Kristi akan kalbari ya fanshi zunubinmu (I Yahaya 2:2) a yanzu shaidan yana kama mutane da **kuskure** ne saboda ba mu yin jayayya da shi wanda ya kamata ya rabu da mu don karmu bata!!

Wani babban makaminmu shine **sunan Yesu**! Almajiran Ubangiji sun dawo daga wa'azinsu da farin ciki sunce wa Ubangijinsu **har aljannu** suna yin masu biyayya ta wurin sunansa" (Luka 10:17) kuma sunyi biyayya da mu kuma!

Akwai dalilai uku a Bebul wanda ya nuna sunan Ubangijinmu Yesu yana da iko a fannin ruhaniya. Farko shi Ubangiji ne a bisa kowane **halitta**. Ta wurinsa ne aka halitta komai, abinda ke bisa da abinda ke kasa, masun ganuwa da marasa ganuwa ko **kursiyai ko masun mulki ko masarauta ko ikoki** wato dukan abubuwa an halicce su ta wurinsa kuma shine (Kolosiyawa 1:16)

Na biyu shi Ubangiji ne ta wurin **gicciye** "Ta wurin daukar kamanin mutuwa watau don ya hallakr da mai ikon mutuwa, watau **Iblis**, tun a mutuwarsa. Ya kuma yantas da duka wadanda suna bauta tun haihuwarsu suke zaman bauta saboda tsoron mutuwa "(Ibraniyawa 2:14-15)

Na uku shi Ubangiji ne **ta wurin nadi** wanda ya je sama yana zaune ga hanun dama na Allah; **kuma mala'iku da masun iko suna binsa** (I Bitrus 3:22)

Tun da shike mu muna biyayya da umurnin nan a madadin Ubangijinmu Yesu cikin rokon mu akan batattu da su sani yantaswa daga ikon aljannu domin suna kalkashin ikonsa ne.

**Kalman Allah** wata babban makami ne wanda zamu yi anfani da shi. Cikin addu'a kamar yadda mun riga mun gani natsoshi na roko wadanda suna da karfi. Ana ma kiran kalman Allah takobi ta ruhaniya (Afisawa 6:17)

Tunda shaidan ya rasa umurnin da ikonsa a kalbari Calvary (Kolossiyawa 2:5) (Ibraniyawa 2:14) abinda yana aiki da shi itace karya. Ko da shike shi kyakyawa ne yana anfani da wannan domin "Yaudaran duniya duka" (Wahayin Yahaya 12:9). Amma kalmar Allah "gaskiya ce" kuma gaskiya yana kada karya **KOWANE LOKACI**. Saboda haka in mun ci gaba da anfani da kalman Allah a yakin mu ta ruhaniya cikin addu'a zamu yi nasara kowane lokaci kuma rayuka zasu yantu!!!

**Yabo** wani makami ne mai iko wanda zamu yi anfani da shi in zamu fara addu'a. in mun fara da yabo sai Allah ya shugabance mu (Zabura 22:3) Menene ya wuce samun kwamanda kyau a fagen fama!!! Babban shaida na ikon yabo shine labarinda yana samuwa cikin II Labarbaru 20 wanda sojojin kasashenda suna gaba da yahuda sun kawo mata farmaki. A lokacin yanayin ya kai intaha har sarki Jehoshaphat ya kira dukan yahudiya su yi addu'a da azumi." Amma sai **LOKACIN** da sun fara wakokin yabo kafin Ubangiji ya kawo wa ya'yan Ammon, Moab, da sauran su kwantan bauna wadanda sun fuskanci yahuda har an bugasu (aya 22)

Wasun mu bamu da masaniya akan yadda yabo yake da iko akan fagen daga na ceton rayuka- ya zamana kenan watakila bamu gane yadda zamu yi anfani da shi ba kenan ko? Muji yadda Francis McGaw ya shaida muhimmin aikin da yabo yake bida a ceton rayuka. Na tuna John yana gaya mini yace cikin wadannan kwanaki in ba a iya ribato rayuka hudu zuwa ga tsira ba in dare ya yi baya iya cin abinci ko barci saboda zai yi ta bimbini yana kuma jin zafin abin a zuciyarsa. Lokacin addu'a kuma sai ya roki Ubangiji ya nuna masa menene wannan cikas take nufi a gareshi. Sai ya

gane cewar rashin yabon nan da bai yi bane a rayuwansa. Wannan umurnin da tana nanata kanta a kalmar Allah shi ya kawo rashin nasara – tabbaci duka kan gani yana da muhimmanci! Idan ya gane kuskurensa ya nemi gafaran zunubansa, yakan samu gafara ta wurin jinin Dan rago. Sai ya ci gaba da neman ruhun yabo ya jagorance shi. Wata baiwane kamar sauran baye-bayen Allah. Yakan nuna kasawarsa har ma yakan ce shi tokan Fure ne makokin sa domin Kristi man-kanshi ne na murna, marmarin nawayan ruhun yabon Kristi shine manufan mu, (wakan Dan ragon na nuna yabo ga Allah domin abin da zai yi) A lokacinda yana **yabon Allah** batattun mutane sukan zo gareshi, yawan masun tuba sai su karu" (Carre 39).

**Azumi** ma yana da iko amma mutane kima ne sukan yi anfani da wannan makamin. "Babban magani ne" muna anfani da shi domin yayata aiki. A nawa gani azumi yana iza ikon addu'a nan da nan!

Dalilin yakin mu ta ruhaniya domin mu yi nasara akan abokan gaban mu kuma azumi yana sa ayi komai da nasara ga abinda Ishaya ya ce Ishaya 58:6 ba wannan irin azumin ne na zabi ba? Ku kwance sarkokin mugunta, ku kwance masun karkiya ku yantar da wadanda ake zalunta, ku kakkarye kowace karkiya?" A wata karo almajiransa suna so su fitar wa wani yaro aljannu basu iya ba, sai Yesu yace masu "Ai irin wannan bay a fita sai da **addu'a da azumi**" (Markus 9:29).

Wani makamin da ake anfani da shi a sashen ruhaniya itace **kauna**. Duk wanda yake kaunar Ubangiji da dukan halittansa ka kuma kaunaci battaun rayuka kamar yadda shi yake yi Wahayin Yahaya 12:11 yace "Sun kuwa yi nasara da shi albarkacin jinin Dan ragon nan da kuma albarkacin maganar da suka shaida domin basu yi tattalin ran su ba har abin ya kai su ga Kisa"

Idan kana da cikakken kaunar wani zaka yi kokari ka cece shi daga jannama. A zahirin gaskiya kauna bata kasawa, yana daurewa cikin kowane hali da bangaskiya cikin kowane hali haka kuma sa zuciya cikin kowane hali da jimiri cikin kowane hali...**BAYA** gazawa (I Korintiyawa 13:7-8) saboda haka idan cikin addu'a muna anfani da makamin da Allah ya bamu fa? II Korintiyawa 10:4-5 ya fadi mana makaman mu na fama bana mutuntaka bane na ikon Allah ne masun rushe makamai masun karfi, muna ka da masu hujjoji cikin zace-zancensu muna rushe kowace ganuwar alfarma mai tare sanin Allah muna kuma jan hankalin kowa ga bautar Almasihu."

Makaman da aka kera na addu'a an tsarrafa sune domin rushe ganuwa alfarwa ya kuma kakkabe kowane tunanin da yana gaba da kaunar Allah. Don haka sai mu maida hankalinmu cikin fagen dagarmu, fagen shine zuciyar. Saboda muna anfani da zuciya ne, zace-zace shi ne tunanin yakin.

Yana da muhimmanci mu gane wannan saboda wanda yana iko da zuciya yana iko da mutumin. Idan shaidan zai ci gaba da yin iko akan zuciyar wadanda basu da ceto zai iya hana su tsira. Hanyan da zai yi kawai shine ya makantar da su daga jin bishara. Saboda duka mutumin da yana cikin tunanin sa mai kyau zai zabi Yesu memakon shaidan, ya zabi aljanna memakon jahannama, a kowane lokaci sai kana cikin tunani mai kyau kafin ka fahinci kome! Sai da aka fitar masa da gungun aljannu kafin ya iya tunanin da zai zabi wani abu don kansa ba wai ya zabi Yesu kadai ba amma marmarin bishara ya zo mashi (Markus 5:15-20)

Mutum wakili ne mai yanci yana iya anfani da abinda ya zama na Allah. Shine mai bauta a duniya, ko ta zunubi ko ta son kai ga kuma nuna bambancin da ke tafe. Dalilin addu'armu ba domin mu dolonci nufin ya kasance ba, ba haka ba domin nufinsa ya kasance a yalwace ba wai hanyan murdawa ba. Don mu kau da kura a idanunsa don ya gani da kyau. Kuma in

babu kame idonsa zai gani da kyau zai kuma san gaskiya, babu murdiya kuma domin dukan hakin aikata kome yana gareshi ne zai iya zaben abinda ya yi dai-dai, addu'ar mu zai cece shi daga hanun miyagu kuma saboda Yesu yayi nasara da mugun za'a iya yin ceto ba tare da wata shakka ba, muna tabatar da tuban wadannan bisa ga tunanin da muke da shi akan addu'oin da muke yi. Addu'a cikin sunan Yesu yana Koran abokan gaban mu daga fegen fama na mutum, a bar mutum ya zabi abinda ransa ke so (Gordon 192-94)

Yanzu mun gane cewar Allah yana anfani da addu'oi saboda ya rushe makamai masu karfi na shaidan, bari mu duba yadda shaidan yana anfani da makamai masu karfi a rayuwan mutane don ya hana su samun tsira. Mafi karfi daga cikin makamai masun karfin sune **MARASA BANGASKIYA**. Babban makami mai karfi shine ka cetu ko kuwa ka bata!! Cikin kristancin ma magabci yana so ya yaudare shi kada ya gaskanta da kalman Allah har ya samu ikon shiga mulkin sa. Amma cikin rashin fahinta kada ya samu tsira har ya karbi Yesu ya zama Ubangijinsa da mai cetonsa.

Da shike rashin bada gaskiya shine zunubinda yana kai mutum jahannama shaidan ya dauke shi ya zama babu sada ya zama da sauki ba wasu dokoki. Babu wani mugun tunanin da zai shafi dokar Allah rayuwa ya zama da sauki kalmar Allah bai hana kome ba. Kamar mutumin nan wanda ya zo wurin Yesu yana tambayansa managarci menene zan yi in gaji rai madawami, Yesu bai fadi masa yadda zai tsira ba. Sai dai yace masa ya rarrabar da arzikinsa ya bai wa gajiyayyu. Amma mai arziki bai yi ninyan haka ba sai ya tafi abinsa yana bakin ciki Yesu ya sani shi mai handama ne kwadayi zai hana shi tsira, sai an rushe kwadayin nan kafin bishara ya zama da nagarta (Markus 10)

Makamai masun karfi na Basamariyan nan shi ne kwadayi. Hiran ta da Yesu na jin dadin rayuwa da tarihi tuna nin ta bai shafi ruhaniya ba. Amma Yesu ya fadi mata a fili cewar ta yi auraya har sau biyar tare da wanda take zama da shi. Sai wannan ya ja hankalinta. Cikin wannan halin ne sai makamai masun karfi nan nata ya ruguje har ta sami tsira (Yahaya 4)

Shaidan yakan yi anfani da **dacin zuciya** domin toshe sanin gaskiya kaunar Allah kuma yana hana mu karban. Misali karamar yariyan da ta saba da maza tun da sai bayan wasu shekaru kafin wani yayi mata wa'azi ta tuba ba zata manta da abinda ya faru da ita a zuciyar taba. Sai an rushe wannan makamai masun karfi da addu'a kafin zata iya karban bisharan sosai. Da wuya a ribato fatsiki ya karbi Kristi – ba wai Allah baya kaunansa bane, ko kuwa ba wai bishara bata da iko bane ko kuwa ana kyaliyane ko lura ba. Amma wannan ya zama makamai masun karfin nan ne.

Wanda sai addu'a da azumi ne zai magance shi da kuma bukatan bangaskiya saboda karya ikon mugun. Mu kan samu karayan zuciya kafin mu yi nasara.

Wata rana ina addu'a saboda wani mutum, na roki Ubangiji ya nuna mini dalilin da ya ki bishara sai na ji kalman nan "iko" ni dai ban gane abinda ake nufi ba. Amma da muka ci gaba da ma'amala da shi sai na gane yana nuna iko wajen jagoranci sai na fahinci kalman nan iko, maka mai masun karfi da ke damunsa shi ne iko, idan a na so ya tuba har ya samu tsira sai an mika shi cikin addu'a!

Ko da shike zurfin bincike makamai masu karfi na wannan littafi bai yi nisa so sai ba. Ina so in yi bayani da wadanda watakila zasu so yin wa wasu masun jarabobi ko ta kwaya, ko giya wannan jaraban ana bukata ka ambata wannan kaitsaye. Wannan anihin damuwan ya zama batanci ne don son zuciya suke dole a nemi yadda za'a kawas da shi domin yana kawo takaici a

rayuwa. Ita jaraba kanta a rufe take kuma tana gina damuwa. Ka roki Ubangiji ya nuna maka wannan tushen damuwan saboda ka yi nasara akanta.

Lokacinda Eddie Smith yana bukata ya san yadda zai taimaki wata wanda yana bata shawara sai ya roki Ubangiji ya nuna masa damuwa ta. Da ya gane sai ta so Eddie ya bayana mata yadda kasashen yammaci suke rawan su, shi Eddie ya bayana mata, sai nan da nan ta barke da hawaye da kururuwa tana cewar "Waya fada maka wannan?" sai ta kwantata labarin ta da alokacinda tana shekaru goma-sha-biyar ta raka abokan ta zuwa wata rawa a kasashen yamma. A can ne ta ga mallamin sunde skul nata yayi tatil ya bugu da giya. Can ne ita ta koma da baya ga nufin Allah tana bayana mashi, idan haka ne akwai Kristanci kuma kana daya daga cikin su" sai tace wa Eddie tunda abin haka ne rayuwa na yana cikin jahannama. Bani da wata bege, ina cikin jarabobin shaye-shayen giya da kwaya. Na yi ta auraya rayuwa babu anfani" sanin anihin damuwanta, ya sa Eddie yayi mata addu'a sai Allah ya yantar da ita (Smith 71-73)

Ina zato akwai daruruwan makamai masun karfi wanda shaidan yana anfani da shi domin yi garkuwa da marasa bangaskiya, amma anihin gaskiyan shine bari mu gane shine akwai dan **mabudi** daya na makamai masun karfi a rayuwan kowane mara bangaskiya, wannan dalilin ne yana hana su karban bishara. Kuma ba'a yakin nan a sakiyar masun zunubi (Ko da shike kowa yana da tashi) yafi so a fuskan mutum guda ana mashi addu'a kuma anihin makamai mai karfi nan ayi anfani da shi ana addu'a watau (damuwan da mutumin yana fuskanta) wannan makami mai karfin nan yana rushe abubuwa, saboda haka idan an rushe wannan damuwan mutumin zai karbi bishara (Luka 11:12-22)

Wata anihin alama na yaki ta ruhaniya duka shine ribato rayuka wannan shine ya nuna muna anfani da **umurnin da muke** da shi cikin Kristi. Ya riga ya bamu darajan ikonsa (Matiyu 16:19) amma dole mu yi anfani da shi. Dai-dai kamar yadda dansanda yakan tsaya a titi yana baiwa motoci hannu su wuce domin wannan umurnin da yake da shi haka masun bangaskiya suna addu'a domin rayuka da shaidan ya makantar dasu su sami yanci. Ikon duhun nan da ke kansa ana karya shi da jinin Kristi ne. kuma idan muna anfani da umurnin mu wanda ke cikinsa ba wani ikon da zai iya yin gwagwarmaya damu……Allah ya kiraye mu domin mu zama kayan aikinsa, ta wurin mu ne zai nuna ikonsa. Bari mu karbi wannan matsayin da bangaskiya mu kuma tsaya da karfi domin hamaya da abokan gaban mu zai yi manya-manya abubuwa ta wurin mu wadanda bamu taba yin mafalkinsa ba. (Epp 108-10)

Halal ne kowane rai na Kristi ne saboda ya biya hakin zunuban su a Kalvary (I Yahaya 2:2). Amma ba halal bane shaidan ya ci gaba da tilasta su su zama fursuna baya so ya bar su su tafi. Zai ci gaba da daure su, sai dai in mun yi anfani da kujeranda an bamu na umurni cikin jinin Kristi mu kuma yantar da su wajen bude idanunsu ta ruhaniya saboda mu wakilansa ne kuma muna karban iko daga wurinsa ne.

Babu wata dalilin da zamu bar wani rai guda daya ya hallaka saboda Kristi ya riga ya dauka fansan su. Kuma dalilin da wani zai shiga wuta shine mu bamu anfani da ikon da aka bamu daga sama don karya karfin mugun mu ci gaba da nacewa cikin addu'a saoda su sami ceto. Iblis ba zai yantar da su ba sai mun roki Ubangiiji.

General Jonathan Wainwright tare da yan fursunan yaki an daure su a kurkukun sibirin na Formosa. Ko da shike yakin ya kare sai Kommandan na Japan ya sani zai iya ce wa shugabanai su sake su ko babu. Amma cikin

karamin lokaci sai jirgin yan fursunan ya sauka a sibirin da labari na nasara. Cewar General Wainwright ya sanar wa kommanda na Japan "Babban kommanda na yayi nasara akan babban kommandan ku. Nine shugaba yanzu". Wannan shine abinda muke sanarwa mutumin nan maikarfi (babban aljannu shugaban rayuka) Babban shugaba na yayi nasara akan babban shugaban ku. Ina neman ka saki wadanda ka bautar da su a jahannama nan da nan" kuma idan mun nace za'a yantar da su a kuma cece su!!!

Na karshe amma muhimmi anfanin addua na ceton raiyuka shi ne mu cigaba **DA KIN** ibilis. An bamu umurni mu sanya garkuwan Allah (Afisawa 6: 10 – 18) don mu iya kin nufin mugun da kuma shirin bilisi. Mu ki mugun ranan nan idan mun bada himma ga ceton rayuka shaidan yakan kawo masaloli masun wuya domin ya samu ya birkice rayuwan mu ko ga wadanda muna yin masu addu'a kokarin sa shine ya mai da mu baya. Abinda ya sa kenan idan wani yana addu'a akan wata masala akan matansa, ko mace tana addu'a akan mijinta ko kuwa tana addu'a don yaranta sai mu gani al'amuran su dada rikicewa memakon yin kyau – shaidan yana so mu dena yin wannan addu'an yana daukan lokaci domin ya hana wadannan rayuka samun tsira!!!

Mu yi tsayayya da Iblis ana nufin kada mu bari al'amura su kasa gudana, watau kada wasu dalilai su hana mu rokon Allah, mu sa ninya cikin addu'ar mu. Idan wani abu makamacin haka ya faru yana zama kamar wuta ne, abinda zaka yi shine ka maida martini da wuta. In kuma abin ya zo na ruwa ana nufi kenan zaka maida martini da ruwa. Ka tabbata duka abin da shaidan yayi kada ka yarda ya shafe ka, ka ci gaba da addu'a akan batattu wanda kana kaunar su domin su kai ga ceto.

Wani abin mammaki na nuna yadda zaka yi sayayya da shaidan game da ceton rayuka yana cikin wadannan shaidu heard by Charles Banchard

wanda ya zama shugaban Kolleji na Wheaton shekaru arba'in da uku. Ya maida wadannan shaidun sun zama zahiri kuma ya rubuta su a littafinsa, Samun Abubuwa Daga Wurin Allah kamar yadda aka ambata a kasa:

*Abokai misalin shekaru biyu da rabi ko uku da suka wuce ina cikin asibiti cikin Filadalfia. Dama ni injiniya ne a Pennsylvania ko da shike ina da mata mai son addu'a kuma ni nayi rayuwana cikin zunubi. A wannan lokaci ina cikin matsananciyar rashin lafiya, sai na zama kamar babu wata anfani kuma. Na kashe abinda ya kai Fam dubu dari.*

*A karshe likitan da yana lura da ni ya fadi wa matata na mutu, amma tace masa "babu bai mutu ba. Kuma ba zai mutu ba na yi masa addu'a na shekara ashirin da bakwai kuma Allah ya fadi mani cewar zai samu ceto". Kana sammani Allah zai barshi ya mutu yanzu bayan na yi masa addu'a kuma Allah yayi mani alkawari cewar zai samu ceto. Kuma bai riga ya tsira ba sai likita ya amsa abaki shikenan. Ni kuma ban san komai game da abinda ke faruwa ba amma "ni na sani ya mutu" An riga an ja labule wanda ke raba wadanda sun mutu da wadanda suke da rai a cikin asibiti.*

*Don mata na ta samu ta gamsu sai aka kawo mata wadanda suna da baiwan warkaswa, aka kawo su da daya-daya sun kai bakwai in da aka ajiye ni, kuma kowane dayan su yakan zo yayi gwaji bisa ga baiwansa na mai wa'azi. Wadannan likitoci bakwai dinnan sun ce na riga na mutu. Nan da nan matana ta durkusa a inda aka kwantar dani ta nace cewar ban mutu ba sai tace ko na mutu Allah zai dawo da ni domin yayi mata alkawari cewar zan samu ceto kuma gashi ban riga na samu ceton ba. Sai sun ce mata sai anjuma ga shi ta fara jin zafin gwiwanta domin tana durkushe a simintin asibiti. Sai ta roki ma'ajiyata su bata matashin-kai sai nas ta kawo mata matashin kan sai ta durkusa a bisa.*

*Sa'a daya, sa'a biyu, sa'a uku suka wuce. Ina kwance a inda aka kare ni. Amace har sa'oi goma-sha-uku suka wuce duka wadannan sa'oi matana tana durkushe a wannan wurin. Sai mutane sun fara lallashin ta domin ta tashi ta tafi: sai ta ce "babu sai ya samu ceto. Allah zai dawo da shi, ko da ya mutu. Bai mutu ba. Ba zai mutu ba sai ya samu ceto."*

*A karshen sa'oi na sha uku sai na bude idanuna sai tace me kake so kaunatace na? sai na ce "ina so in tafi gida" sai tace "zaka tafi gida". Da ta bada shawara cewar akai ni gida sai likitoci suka cika da mammaki suka daga hanuwan su sama don mammaki. Sai suka ce don me ake son "kasha shi gashi yana da rai". Tace kun gama aikin ku. Kun ce ya riga ya mutu to zan kai shi gida.*

*Ga shi yanzu ina da nauyin da ya kai 246. Har ina tuka jirgin da yafi gudu duka a Pennysylvania Lena. Na fita in tafi inda mutane suna hutu a Minneapolis ina shaida masu abinda Yesu yana iya yi. Kuma ina da farin cikin shaida maku abinda Yesu yana yi (Blanchard 94-95).*

Akwai dalilai biyu kawai wanda zai hana amshin addu'a don ceton batattu tana yuwa akwai zunubi ko kuwa wanda yana addu'a din bai gaskanta da addu'an ba. Ko kuwa shaidan yana hana amsan addu'an zuwa don haka in ka shirya kanka shike nan (Yahaya 15:7) ka ci gaba da addu'a amsa zai zo don shaidan ba zai hana amsan zuwa sam-sam ba, dole mu yi ta addu'a na yaki.

Ku sani cikin kowane yaki dole a yi shiri. Soja baya zuwa ko'ina yana ta harbi ko menene da ya samu ba. Haka ma yake cikin addu'a yaki don ceton rayuka, muna bukatan karfi.

Karshen dabara ya rage na Ikklisiya don ta bada kanta kamar yadda ya kamata don su ci gaba da addu'a. Ikklisiyoyi na da' suka yi haka. "Duka suka ci gaba da addu'a da manufa daya da godiya (Ayukan Manzani 1:14)

zasu fitar da amsa mai kyau a wannan rana aka kara masun bangaskiya har dubu-uku (Ayukan Manzani 2:41) Yawancin su da suka saurari kalman sun bada gaskiya kuma yawan masun bi sun kai dubu-biyar (Ayukan Manzani 4:4)

Akwai taron addu'a an ce "Bayan sunyi addu'a wurin da suka tattare ya raurawa sai duka aka cika su da ruhu mai tsarki suka yi ta fadar maganar Allah gaba gadi "(Ayukan Manzani 4:31) "tare da ribato rayuka masun yawar "taron jama'a maza da mata sun karu" (Ayukan Manzani 5:14) "maganar Allah kuwa sai kara habaka take yi yawan masu birnin urushalima sai karuwa suke ta yi "(Ayukan Manzani 6:7) "Duk mutanen Lidda da na kasar sarona kuwa suke ganshi suka juyo ga Ubagiji "(Ayukan Mazani 9:35) kuma akwai wurare da yawa cikin littafin Ayukan manzani wanda ya bayana kusan abu daya haka. Idan ikilisiya ayau zata bi wannan gur bi na addu'a irin na kristan da zasu yi aikin bishara daidai kamar mutanen su kuma rabato rayuka.

Wata sabuwar hanyan dabaran shine a kasance da kungiyoyi addu'a, kamata yayi ko wane ikilisiya ta kasance da kungiyan asddu'a zai zama kamar ajujuwan sonde skul ko kungiyoyin addu'a ta gidaje, tunda suna haduwa a kowane lokaci. Zasu iya nacewa suna dukufa cikin addu'a akungiyance domin batattun rayukan da sun sanya agaba sunance cikin addua'a sosai don wadannan batattun su karbi Kristi.

Evelyn Christenson ta yaba wa addu'a ta naciya,domin ya zama daya daga roko mai karfi wanda yana aiki da sauri ya zama wata hikima na shirin addu,a don bishra.

Wannan ya kunshi abubuwa kashi uku, ya zamana Krista suna da manufan almajirantar da juna su kuma rika yin addu'a kowace mako don rayukan guda tara. Ta bayana yadda wannan addu'an zai ribambanya cikin

aikin inji Billy Graham awa’azinsa na bainin jama,a a England wanda ya ribambanya da hayayyafa Billy Graham ya taba tara mutane sama da 90,000 a wa’azin san a 1984 wanda yayi a filin mishan a England Krista kuma suka taru sosai ya kai matsayin da aka raba kungiyoyin kashi uku su ci gaba da addu’a kafin lokacin wa’a zin. Kuma ko wane mutane uku Krista suka zabi mutane uku wanda su ba Krista ba sai su hada hannu domin addu’a, sun yi addu’a na tsawon shekara daya kafin a fara wannan,sun nemi fuskar Yesu. A Janairu 1989, ankarfafa. Cikin mujalla a ninka wadannan rokon sosai don mai wa’azin nan Billy awannan shekaran 1989 sai Mishan na England II sun fitar da rohoton cewar mutanen da ana addu’a sabo da su yawancin su sun karbi Kristi inji masun addu’an, kafin zuwan Billy an samu iklisiyoyi sama da 7,000 wanda akwai sabobin tuba a cikin su ninkin ba ninki saboda fitan aikin mishan na Billy a England a ‘89. An samu wannan nasara ne don an gane iko yadda za’a yaki shaidan don ceton rayukan mutane a dukan kasan (Christenson 110)!

Kasancewa da abokin addu’a wata sabuwar hanyan dabara ne cikin yin addu’a don rayuka su tsera yana da sauki ku zama kungiya mutum biyu ko uku, da aje a tara mutane da yawa. Mutum da matansa zasu iya zama kungiya ya fi kyau don akwai zumunci, kullum suna tare za’a kuma iya zama makwabta, ko abokai da dai sauransu. Kuma kowane dan kungiya zai yi aiki. Yesu yace za’a amsa addu’ansu (Matiyu 18:19).

Zan ambata dabara na karshe wanda yana aiki sosai akan addu’an mutum daya karbabe na farko ka zana sunayen wadanda zaka yi masu addu’a tare da na dubban wasun da sun riga sun yi anfani da shi na tsawon shekara daya amma basu ga wani mutum daya ya zo wurin Kristi ba. Ina barin wannan labarin da na samu albarka a ciki. Ina fatan zaku samu haka.

*Wasu shekarun da suka wuce a wata sifirin wani mai suna Illinois mutum mai gaskiya ya kira wasu tare da shi sai ya kawo masu shawara. Idan kun koma gida da yammacin yau ku rubuta sunayen wadanda kuna bukata su tsira duk wanda ruhu ya bisheku ku sa sunansa. Wadanda kuna bukata ku yi masu addu'a kuna ambata sunayensu, sau uku a rana daya don su samu ceto ka yi iyakan kokarinka ka ga sun tuba.*

*A cikin manzanin Sifirin nan a lokacin akwai wata matan da take zama a wurin. A gaskiya cikin rayuwan ta bata da wata begen warkewa a rashin lafiyan ta don ta kai shekaru bakwai tana kwance akan gado. Amma tana addu'a don marasa bangaskiya ga Kristi ta yi ko kari don mutane su cetu daga ikon Iblis. Tana cikin haka sai ga labari daga mutanen gidan ta cewar an shirya wata addu'a don batattu, sai tace wannan shine abinda ya kamata in rika yi, kuma tana iya motsa hanun damanta, sai ta ja wata teburi wanda yana gefen gadonta. Ta nemi alkalamin rubutu, sai ta zana sunayen mutane hamsin da bakwai. Ta fara wa kowane dayan su addu'a tana ambata sunayensu da daya-daya sau uku a kowace rana. Sai ta rubuta wasika zuwa ga sauran masun bi wanda ta sansu tana karfafa su domin suyi wa wadannan mutane Magana watau su karfafa su don su tuba su bada gaskiya ga Kristi. Ita mara lafiyan tsayayya ce sosai ta dogara ga Allah tana roko don marasa bangaskiya. A cikin dan lokaci kima sai mutanen nan hamsin da bakwai duka sun tuba sun karbi Kristi ya zama Ubangijin su da mai ceton su. (Mc Clure 124-25)*

# BABI 6

## SHAIDAR KANKA

Na koyas da wannan manufan a Ikklisiyar Crestview Baptist Farmerville Louisiana a Mayu 2002 dan'uwa Pasto Wayne Whiteside ya rubuta mani wasika cewar "mun gani makamai masun karfi wanda mutane sun saba aikatawa a rayuwansu yanzu suna barinsa don koyaswa ya shiga zuciyarsu suna dawowa wurin Kristi don addu'an da ake yi don batattu yana shafansu.

Wayne yana da hakin da Allah ya danka masa watau yana shaida Kristi ga yan kurkuku wanda an yanke masu hukuncin kisa kuma yakan kashe yawan lokacinsa a wurin kokarinsa shine ya jawo su zuwa ga sanin Kristi. Ya ci gaba da bada labarin sa. "Babban nasara da yana samu shine akwai wani dan kurkuku wanda yana fuskantar harbi a Huntsville, Texas. Wannan mutumin musulmi ne kuma ya bada kai sosai a musulci kuma mai adalci ne fiye da Krista, na dade ina aiki tare da shi na kimanin shekaru biyu, ina ta yin masa wa'azi watau ina shaida masa bishara, kuma na sa Ikklisiya suna addu'a dominsa, kuma duka banza, domin duk lokacin da in na rubuta masa wasika yakan karasa da Allah ya kasance da kai, duk da wannan ban taba karaya akan wannan masala ba.

Sa'anan, wajen watanni biyu kafin lokacin da za'a zartadda da shi a satumba 2002, na karfafa Ikklisiyarmu da suyi addu'a ta musamman domin daddaure karfafan mutumin nan ta addinin karya da kuma rokon jinin Kristi a bisansa. Nan take aka samu change. Ya fara bayana da cewa Yesu malami ne mai kyau sa'anan wasikarsa ta karasa da cewan "Allah ya bi tare da mu".

Ya gayyace ni da in kasance a wurin zartadda shi. Na yi yar tafiya zuwa Huntsville don in ganshi na karshe. Zuciyana ta motsa sosai sa'an da yayi mani tambaya cewa, 'Me zanyi domin in amince da Kristi don ceto?' A

karfe 3:05 na yamma ya roke Ubangiji Yesu ya cece shi. Bayan awoyi hamsin da daya da mintoci goma-sha-biyu ya mutu. Sauran awoyi biyu kawai kafin a zartadda shi, sai ya kyafta mani ido yace, 'ina kaunarka kuma ina jiranka a mulkin sama.' Kalmomi na karshen da yayi a duniya sune: 'Allah yana gafartawa. Mai girma ne duka kuma!' ya kuma mutu da salama a fuskarsa, har gandurobobin suka yi Magana akai.

Duka abinda muna kokarin yi cikin karfin mu domin mu jawo mutane zuwa ga Kristi zai zama banza in muna tunani cewar wanda ya riga ya cusa kansa akan addini kuma yayi karfi a ciki yana da wuya mu rinjaye shi sai dai mun yi addu'a cikin jinin Yesu kadai. Shine zamu ga yadda za'a kakarye karfin magabci da kuma yadda za'a bude kofofi domin bishara ta shiga tunda ya tambaya yaya zanyi in samu tsira. Ya shiga aljanna yau domin mun koyi yadda za'a yi wa batattau addu'a, musamman akan yadda za'a daure mai karfin nan kamar yadda Yesu ya fadi cikin Markus 3:37 mun gode domin kayi Magana da mu asake kuma ka fede gaskiyar maganar ga jama'a. A karshe Ubangiji ya baka nasara cikin girbinsa.

In mun fara addu'a domin wani ya samu ceto Allah yakan ja layi akan wannan mutumin, ta wurin wannan layin sai a shigo ciki. Abinda ya faru da Ricky Gresham lokacin da matansa Helen da Paston ta Mickey Hudnall sun fara addu'a dominsa. Ku ji labarin bangaren Rick. Sakanin watan Febairu da maris na 1990 a wadannan kwanaki na samu kaina ckin bakin ciki, wani miskila ne wanda ban taba shiga irin wannan rayuwa ba. Ko da shike ban gane a wancan lokacin ba cewar ruhu mai tsarki ne ya daure ni. Ban san abinda ke faruwa ba amma abinda na sani shine duk inda na juya a wadancan watani biyun duka abinda nake ji ko gani shine abinda ya shafi Allah. Sai ya zama har kowane rana in na falka akwai Allah mutanen da

daman da na sansu shekaru da dama yanzu suna mani Magana akan Ubangiji sai abin ya zama ba yadda zan boye ko ina.

Sai na tuna wata rana Aminina na kusa muna karatu a motansa, sai wani abokinsa ya tsayar da mu a gefen hanya. Sai wannan mutum ya hau motan da muke ya zauna a gefen na sai ya ci gaba da Magana. Cikin tattaunawar mu sai ya fara wa amini na maganar Ubangiji, yana karfafa shi ya karbi Ubangiji a matsayin mai cetonsa. Har yanzu na ci gaba da sauraran maganar Allah. Sai ya zamana ba yadda zan boye kai na. na ci gaba da zama a wannan motan ba wani Magana kuma sai abin ya zama mani ina kuma marmarin jin kalmar Allah, amma bukatan aminina ya ci gaba da tuki. A karshe bayan wannan abubuwan da suka faru duka a sa'a daya da (minti biyar) sai ya ci gaba da tuki.

Da kwanaki suka ci gaba da wucewa sai Allah ya nuna gaskiyarsa cikin aiki. A wancan lokaci ni da kai na ma'aikaci ne a wata ma'ikata na karafuna. Kuma akwai wani bakin fata wanda zai zo yayi Magana da ni. Cikin wannan yanayi wanda na riga na rinjayu sai ya fito daga ma'aikatan. A nawa fahariya, nace ba zan yi wata tambaya game da Ubangiji ba. A karshe na mike a tsaye cikin karfin zuciya na yi masa tambaya akan Ubangiji. Ko da shike ba wai ina marmarin jin amsan bane.

Sai yace bani dan lokaci sai ya koma cikin motansa, sai na gani yana dawowa da Bebul din yana karanta mani wasu zantatuka. Ban ma fahinci abinda yana shaida mani ba, amma akwai wani abu daya da ni yau shine ban manta ba: "za'a maya haihuwanku!" Ya nanata wannan kalman sau da sau. Wannan kalma bai rabu da zuciya na ba!

A dai-dai wannan lokaci akwai abinda yana jan hankalina zuwa ga kalmar Allah. Kuma ina wani fahariya ne in tamabayi wani Bebul sai na duba wata fatsaran Bebul (Encyclopedia) akwai hoton Kristi a wurin a gicciye sai

zuciyana ya koma akan wannan hoton Ubangiji sai da ya kai wani matsayi, **kowane dare sai in sulale zuwa wurin wannan hoton ina ta kallaon hoton**.

Bayan makoni kima sai na fara kokarin canza rayuwa na. na kai wani matsayi a rayuwana ina gani kome la'ana ne wasu kalmomi a wurina la'ana ne. sai na yi kokari domin in bar wannan tunani amma ban iya ba, wannan tunanin ya dauke hankali na.

A karshe wata rana a wurin aiki lokacin da ina kadaice sai na yi wa Allah Magana cewar ba zan iya yin wannan rayuwa ba ka taimake ni Allah. Ni dai ban gane abinda Yesu yayi mani akan gicciye ba, amma ka nuna mini na yarda zan bi ka'. Tun daga wancan rana rayuwa na ya tsauya. Ba wai ina la'antar al'amurana kadai ba amma na watsar da su. Ya zama kamar dama babu wancan tunanin a wurina.

Sai ya zama dole in fadi wa wani abinda ke faruwa da ni, sai na fadi wa Pasto ko zan gaya wa Ikklisiya wani abu. Duka abinda ina nufin fadi shi ne Allah ya kawo ni a kaunatacen wurin Ubangijin mu Yesu kuma zan bishi akarshen rayuwa na abinda ban sani ba shine cikin watani biyu nan matana tana mini addu'a da Paston ta. Abinda ina dandana a rayuwa ta amsan addu'arsu ne, yanzu dai na sani amintatcen addu'a ne ya cece ni an bar ni ne in dandana wannan yanayi domin in dawo ga Ubangiji! A yanzu haka ni Pasto ne na Ikklisiya, kuma ina ci gaba da dandana alherin Allah."

Idan mun yi addu'a don Allah ya cece wani, dole ya kamata mu roki Allah don ya ja hankalinsa zuwa gareshi. Wesley Deuwel yace "addu'oin mutane da yawa yakan samo amsashi don shirin Allah haka. Kuma mu sani Allah ba ya jujjuya mtutm kamar masa akasko ba. Yana anfani damu, yakan lallashi mutane a hanyoyi dabam-dabam yakan kawo wasu dabarunsa a tunanin mutane" (Deuwel 262) ko da shike wata matsi yakan zama kamar

ciwo! Dama wannan shine masalan Tony Fontenot." An haife ni cikin iyalin Krista, kuma akwai wadanda suna mini addu'a cikin gidan mu, mutane kamar mahaifinta da mamanta da dai sauransu da shike suna mini addu'a sai in shiga gantalina. Amma in Allah yana so ya bamu horo,kuma muka ci gaba da bin nufinmu zai barmu cikin hatsarin dan mu horu kafin **ya dawo da mu!!**

Allah ya dawo da hankalina ran 22 ga Mayu 1982. Na gama feshi kenan a gonar waken-soya na sai na hau jirgin sama zan koma masauki ke nan sai jirgin sama na ya samu hatsari a sakanin wasu kebabun itatuwa nan take sai wuta ya amsa. Sai ga wuta yana kewaye da ni!!. Bayan na mirgina a kasa na dauko abin kashe gobara da na mike a tsaye sai na gane rigana ya kone duka har fatan hannuna ya daye ya kwanta akan yatsun kamar gidan gizo-gizo daya idona na dama a makance yake kuma ruwa yana tsiyayewa a jikina – na sani a daure nike.

Sai na fara ihu neman taimako amma ba wanda zai ji, sai na fara gudu har na gaji bana iya gudun kuma ba sai na kwanta a tushen wata itaciya a wannan lokaci ne na fara addu'a. Na roki Allah da ya kawo wani domin ya ganni don kada in mutu anan. Sai na fara ganin wasu alamu na ji kamar wani abu ya fado kamar wani ya zo ya dauke ni sai na fara jin karfi a jikina sai na yi wuf na tashi na fara gudu a karshe duka sai na hangi wani a kori-kura. Sai na zo kusa da akori-kuran ina ta ihu ina neman taimako. Mutumin da yana aiki ya daga ido sai ya ga yanayi na sai ya dauke ni a guje zuwa asibiti kafin hankalina ya kwanta na kuma sani ni John Sealey Burn Center Galveston, Texas ne wanda na kone kuma sai aka kai ni wurin masun kuna, na Texas na kwanta a wurin, na wata biyu, inda ake lura da marasa lafiya.

Ta wurin wadannan wahalu duka a karshe Allah ya ja hankali na a Nuwamba 1982. Wanda dan'uwa Lee Thomas a wa'azinsa na taron falkawa

a Ikklisiyar Baptist ta kauyen India. A wannan lokacin ne ya shaida mani bishara kuma na gaskanta da Kristi kuma na samu ceto. Ya ce mani, Tony wannan hatsarin jirgin saman da ya faru nan ya zama wata babban dalili ne a rayuwanka, ta wurin haka zaka sadu da Ubangiji. Na yarda!!

Oswald Chambers yace idan muna addu'a don wasu, ruhu Allah yana aiki cikin lamirin zuciyarsu wanda mu bamu da wata masaniya akan ta, kuma addu'an da muna yi wa marasa bi, sai ruhun Allah ya ziyarce su har basu samun salama, irin wannan ne yakan lalatar da shirin shaidan da ikonsa. Haka yakan fara kadan-kadan cikin matakin farko idan dalilin bai hada da hasken ruhu mai tsarki ba, ba zamu bi nufin Allah ba, amma idan addu'a ya hadu da hasken Allah yana rushe mulkin shaidan (Chambers 102-03). Wannan shine halin da Jacob William ya samu kansa a ciki. Ko da shike shi yana cikin halin gaskantawa ne wanda ya dade, lokacin da iyalansa da abokansa suka damu da shi sun dukufa cikin addu'a domin ya samu ceto. Ku ji labarinsa ya ce, Ina cikin jin dadin duniya na sai muka tafi Ikklisiya Baptist ta Westwood. Sai kawai nan da nan na tabbatar da cewar Ubangiji yana bukata na, amma ina ta kokuwa a zuciya ta game da abubuwan duniya, duk lokacin da, idan mun tafi sujada, na kan yi kokuwan nan a zuciya ta, sai da na dauki lokaci ina wannan tunanin, sai marmarin zuwa sujada ya kare, bana so in tafi Ikklisiya. Mahaifiya ta, ta ci gaba da matsa mani in tafi Ikklisiya. Sai na fara gujewa zaman gida. Kuma ina da wata muguwar budurwa, sai abubuwa sun dada rincabewa.

Ya kai wata mataki wanda mutanen gidan mu sun fara damuwa a kaina. Wannan ya faru a lokacin krismeti ne har ya kai sun fara addu'a sosai domina suna bukata in sadu da Kristi. Sai na fara zuwa gida amman da dare ne nake shiga gidan don kada iyayena su ganni wani lokaci mahaifi na zai jira ni don yayi Magana da ni akan rayuwan ruhaniya na. na ci gaba da fadi

masa cewar ina da ceto tun ina shekara sha uku amma duka mun sani abinda nake fadi ba gaskiya bane.

A wadannan lokatai ni da kaina na tabbata ina bukatan ceto don tunanin ya dame ni a zuciya. Amma na ci gaba da tsayayya da shi. A karshe cikin watan biyu ban iya daurewa kuma ba – na roki Allah ya cece ni. Daga baya na ji mutane da yawa suna addu'a domina, a lokacin da hankali na ya birkita ba wai iyayena ne kadai suke addu'a ba yawanci mutane cikin Ikklisiyan mu. Kanina ya roki kungiyan matasa suna addu'a domina. Na yi farin ciki Allah ya amsa addu'arsu.

Rachele Barrentine tana cikin yanayin bukata sosai don tace mini in taimake ta addu'a akan mai gidanta ya samu ceto. Ta ce yawan shaye-shayen sa, da caca da kuma ya kan kwana a waje, baya zuwa gida tana addu'a amma kamar ba anfani. Haka magabci yana so mu yi tunani don mu dena addu'an. A wani aiki Allah shine yakan kawo wa mutum tabbacin ceton sa a zuciya a lokacin da kokarin mu ya kasa. Wanna shine ma ya faru da Jimbo Barrentine. "Ko da dai na yi girma a Ikklisiyar Baptist ta Westwood na cika kaina da wasu abubuwa har Allah baya tare da ni. Ina rigima sosai. Bayan aurena da kuma samun dana na farko sai na sake koma Ikklisiya. Amma ina tafiya a nufin jiki ne. ban natsu ba ina shagali na har mun rabu da matana, kuma ina cikin makuwa bayan rasa iyali na ne rayuwata a duniya ya zama abin tausayi.

Na yi tunani cewar rayuwa zai yi kyau in na auri Rachele, amma ba haka ba, bai zama da kyau ba, abin ya dade lalacewa, ita ta tsira. Rayuwa na ya dada muni domin nakan kwana a waje ina ta shaye-shaye ina ayukan masha'a, ban san lokacin da ita iayalina ta tuba ba don lokacinda mun rabu sai ita ta mika kanta ga Ubangiji.

Sai wani ran talata ina ta rayuna na a duniya watau 13 ga maris 2001 sai na tafi gida, washe-gari laraba da safe sai na yi tunani cewar ya kamata in bari Allah ya mallake ni; Ban iya ci gaba da rayuwa kamar yadda na saba ba. Sai na tafi Ikklisiya don in yi Magana da dan'uwa Lee don neman ceto, amma baya gari. Sai na ja motana zuwa gidan kawuna Bob da tunani zai taimake ni don shi mai wa'azi ne kuma na sani shi da inna Faye suna addu'a domina na wasu shekaru.

Inna faye (Yar'uwar mamata ce) ta ce da ni mijinta ne da ta rabu da ni da dadewa sai ina da farin ciki don Rachele bata rabu da ni ba har zuwa wannan Laraba da safe, a wannan ranan ne na mika kaina ga Kristi ya cece ni. Sai abin al'ajibi ya sauya rayuwana.

Hawaye yana ta sauka don addu'an da ake ta yi mani wata kila sune masun addu'a da karfi!! Na gane suna da karfi a cikin bin Ubangiji a lokacin da suna gudanar da wata hidimar janai'za ne a Louisiana na wata mata wanda tana aikin Pasto da dadewa shekaru da dama cikin wani gari a Texas. A wannan jana'iza akwai wani mutum a wurin ya tako zuwa wurina ya mika mani hanu don mu sha hanu da shi, yace baka sanni ba ko ka sanni? Sai nace babu kuma na sani ban san shi ba. Sai yace "ina zama a cikin Buna a nan Texas kuma na karanta jarida cewar Lee Thomas ne zai gudanar da wannan janai'izan. Na zo in gani ko kai ne Lee Thomas tunani na kenan". Ya bani wannan labarin: "sai nace masa suna na Yakubu Lynch ne anyi reno na a gidan Krista amma lokacin da nake zama a Orange, Texas ni shahararen mashayi ne bana iya zama a wurin aiki. Wata rana ina zaune a dakina ina fama da shaye-shaye na har na rude akan rayuwa sai aka kwankwasa kofa na.

Na ce maka ka shigo nan da nan da ka shigo gida na sai naga hawaye yana zuba a idon ka sai kace dani Yesu yana kauna ta yana so ya cece ni amma giya ya bata rayuwanka har ka ki kyautar Allah ta ceto.

Ka durkusa a gefen kujera na ka zubar da hawaye a idanunka kana roko na in gaskata da Kristi don in tsira.  A ranan na tsoku a zuciya ta har na so in mika kai, amma ban iya ba don giya yana mallaka ta.

Na dauki shekaru uku wannan al'amuran yana damuna musamman hawayen nan ya tada hankali na ban taba wuce wata rana ba tare da tuna wannan al'amuran ba yadda ka durkusa a gaba na kana kuma roko na da hawaye. Bayan na yi jayya da Allah na shekara uku na tuba kuma Allah ya cece ni kuma ya kira ni don in zama mai wa'azi, kuma na dauki shekaru ina aikin wa'azi. Na tabbata da baka zo gidana ba dana bata watakila da ban san Allah ba kila da na riga na mutu har na shiga wuta."

Ya dauki George Muller shekaru sittin yana addu'a kafin abokinsa ya karbi Kristi. Kuka da hawaye na addu'a ya kai shekara uku kafin Yakubu Lynch ya karbi Kristi. Jabez Carey kuma ya karbi Kristi a sa'oi biyu yayin da mutane dubu biyu sun yimasa addu'a, wannan ya tabbatar mana cewar addu'a wanda ake yi a hada kai yana da karfi don ceton batattu.

Ga wata hanyan da Mike Doles ya sami ceto. Ga labarinsa: "Na yi girma a Ikklisiyar Baptist ta sabon bege, amma ban gaskanta da Ubangiji ya cece ni ba. Ni dai naga abokan makaranta na sun shiga Ikklisiya ni ban shiga ba. Na ga yan'uwana maza da mata sun shiga Ikklisiya ni dai ban shiga ba. Na gaskanta abinda ake fadi cewar akwai rai madawami, na kuma sani bangaskiya ga Kristi shine muhimmin abu amma ban aikata haka ba.

Ko da shike mahaifiyata da tana addu'a domina amma ba abinda ya faru sai ran da Pasto yace wa mutane, kowa ya rubuta sunan wanda zaka rika yin masa addu'a domin ya tsira. Daga baya ya fadi mani cewar ya karbi

sunana a wurin mutane goma-sha-takwas wanda sunce suna mini addu'a. bayan dan lokaci kima sun yi addu'a domina, sai na fara gane cewar bana bin abinda ana koyaswa ina tunani ne kawai, wannan tunanin ta kai ni binciken maganar Allah watau ina karanta Bebul ina kwatatanta da kaina ina cewa Ubangiji ka nuna mini abinda kake so in yi maka.

Da ma na riga na fara zuwa Ikklisiya ran lahadi don sujada safe sai ran 1, maris 1998  mako biyu bayan wadannan mutane sun fara addu'a domina, sai Ubangiji ya fadi mani cewar ka bar bautar ido, ka dauki mataki mai kyau shi zai gama saura wannan shine farkon mika wa Ubangiji rayuwa na. ko da shike na kashe shekaru arba'in da tara na rayuwa na ina tsayayya da Ubangiji, yanzu na san hakina na Krista shine in yi anfani da dukiya na don taimako wajen shelar bishara. Kuma wannan zan yi anfani da dukan aninda nake da shi, da kuma zarafin da Ubangiji ya bani!

# BABI 7

# YIN ALKAWARI

Wannan littafi ba a rubuta don a ajiye a kanta kawai ba. Amma don a karanta kuma ya ratsa zuciya, ya kuma huda gaskiyar dake cikin yanayin. Ya kamata ka sani kadaran wani yana hanunka wani zai iya mutuwa ya tafi jahannama in baka yi addu'a ba!! Andrews Murray yace ninyan mu ya zama dole don mu ceci rayuka. Dubban mutane suna hallaka a duniya begen shi ne ayi ta rokon Allah don ya cece rayuka, wace aikin kauna ne kayi har ka kwatanta kamar babu anfani, saboda kome karamin roko anan duniya yakan ceci rai, babu abinda yafi daraja kamar yadda Kristi ya saye mu da jininsa mai tamani, ta wurin wannan ikon ne zamu iya ribato kowane rai rokon mu" (Murray 112)

Addu'a ta bari wannan littafi zai zama abokin hiranka yayin da kana lura da gaskiyar da ke cikin ta zai zama babban abin addu'a don batattun rayuka su kai ga tsira kamar yadda Allah yake bukata. Kai ma kayi aikin. Yayin da kake karanta wannan waken Sandra Goodwin ina fata zuciyarka zai tsoku kace nima zan yi aiki".

### TAFIYA DA GUIWA NA

Jiya na yi tafiya da dare
Zuwa kasan da ke ketaren teku
Ban tafi da jirgin ruwa ko
Sama ba, da Guiwa na

Na ga mutane da yawa a can
Wadanda suna daure da zunubansu
Yesu yace mini in tafi
Akwai rayukan da zan ceta.

Amma nace Yesu bazan iya tafi
Ya kasan da ke ketaren teku ba"
Ya amsa maza zaka iya
Da guiwanka zaka tafi.

Yace ka yi addu'a zan biya bukata
Ka yi kira zan ji
Ya rage naka ne ka
Damu da batattun rayuka
Na kusa da nesa.

Saboda haka na dukafa cikin addu'a
Na bada lokacina na hutu
Tare da nufin mai ceto na
Na yi tafiya da guiwana
Ina ta bauta a gonan.

Nace "I Ubangiji zan yi aikin
Ina so in faranta ran ka
Zan ji kiranka in kuma tafi
Ta wurin tafiya da guiwa na".

(Lundstrom 207-08)

Nufin Allah ne mutane su kasance da nauyin zuciyar game da batattun rayukan da suna hallaka cikin jahannama ya kamata dinbin mutanen Allah su zama masun addu'a da roko don ceton batattu rayuka. Zan yi babban godiya in har zaka sanar da ni cewar ka hada hannu da ni ciki hidiman nan. Mai karfi wanda dukan mu muna addu'a domin marasa bi!!

Kuma in akwai wani da kana bukata ya kubuta daga hallaka sai ka aika da sunan sa/ta ka kuma sanar da ni dangantakar mutumin da kai kanka ka kuma sanar da ni labarin mutumin, sa'anan zan ci gaba da addu'a tare da kai bisa ga alkawarin Ubangiji cikin Matiyu 18:19. Amma ina cewar haka ne domin in kana da wani wanda ka kosa kuma kana addu'a dominsa bisa ga dabarun da na zana su a wannan littafin. Zan kuma bukaceka ka sanar da ni yadda Allah yake aikinsa a yanayin da muke addu'a musamman akan karban ceton sa/ta!

## TSARIN ADDU'A TA

(I Samaila 12:23). "Amma ni kaina. Allah ya sawwaka in yi wa Ubangiji **zunubi** ta wurin **fasa yin addu'a ga** Ubangiji domin ku".

1. ………………………………………………………………………………………….
2. ………………………………………………………………………………………….
3. ………………………………………………………………………………………….
4. ………………………………………………………………………………………….
5. ………………………………………………………………………………………….
6. ………………………………………………………………………………………….
7. ………………………………………………………………………………………….
8. ………………………………………………………………………………………….
9. ………………………………………………………………………………………….
10. ………………………………………………………………………………………….
11. ………………………………………………………………………………………….
12. ………………………………………………………………………………………….
13. ………………………………………………………………………………………….
14. ………………………………………………………………………………………….
15. ………………………………………………………………………………………….
16. ………………………………………………………………………………………….
17. ………………………………………………………………………………………….
18. ………………………………………………………………………………………….
19. ………………………………………………………………………………………….
20. ………………………………………………………………………………………….
21. ………………………………………………………………………………………….
22. ………………………………………………………………………………………….
23. ………………………………………………………………………………………….
24. ………………………………………………………………………………………….

## AIKI


Billheimer Paul E. Shawo kan kadara. Minneapolis: Gidan Bethany 1982.

Blanchard, Charles Samun abubuwa wurin Allah. Chicago: Moody 1984.

Carre, E. G . Addu'a Hyde. South Plainsfield: Bridge, n.d.

Chadwick, Samuel. Hanya zuwa Fentakos. Fort Washington: CLC, 2001.

Chafer Lewis. S. Bishara ta gaskiya. Findley: Durham, 1919.

Chambers, Oswald. Idan zaka nema. Alexandrai: Lamplighter, n.d.

Christenson, Evelyn. Sakamakon yakan duhu. Wheaton: Victor, 1990

Cymbala, Jim. Sabuwar iska da sabuwar wuta. Grand Rapids: Zondervan, 1997

Deuwel, Wesley. Addu'an da tafi karbuwa. Grand Rapids: Ashbury, 1990.

Dunn, Ronald. Kada ka tsaya kawai kayi addu'a akan wani abu. Nashville: Nelson, 1992

Eastman, Dick. Ba hanya mai sauki. Grand Rapid: 1971

Edwards, Brian. Falkaswa. Durham: Evangelical, 1990

Epp, Theodore H. Addu'a da iko. Lincoln: Bible Broadcast, 1965

Finney, Charles G. Falkaswar addini. Old Tappan: Revell, n.d.

Charles G. Finney: An Autobiography. Westwood: Revell 1876.

Gordon, A.J. Ruhu mai tsarki cikin manufa. New York: Revell, 1893.

Godon, S.D. Anatsu shiru don addu'a. New York: Revell, 1903

Huegel, E.J. Zuzzurfan asirin addu'a. Grand Rapids: Zondervan, 1959.

Lundstrom, Lowell. Yadda za'a yi addu'a da iko a samu amsa. Sisseton: Lundstrom Ministries, 1981

Matthews, R. Arthur. An Haifa don yaki. Wheaton: Shaw, 1978.

McClure James G.K. Addu'an roko. Chicago Moody, 1902.

Murray, Andrew. Hidima ta roke-roke. Old Tappan: Revell n.d.

Newell, Philip. Falkawa akan sharudar Allah. Chicago Moody, 1959.

Penn-Lewis, Jessie. Bishara da addu'a. Dorset Overcomer, n.d.

Pierson, A.T. George Muller of Bristol. Old Tappan: Revell, 1899.

Ravenhill, Leonard Falkarwa a nufin Allah. Minneapolis: Bethany House, 1986

Smith, Eddie. Roko don wasu. Houston: SpiriTruth, 1998.

Spurgeon, Charles. Sauyawana. Springdale: Whitaker, 1996.

Jawabai sha biyu akan addu'a. Grand Rapids: Baker, 1990.

Steer, Roger: Murna cikin Allah na George. Muller Wheaton: Shaw, 1981.

## BALA’I

Kimanin mutane 1,836 suna mutuwa a sakamakon mahaukaciyar guguwan da ana kira mafi munin bala’in da ta taba buga Amirka wanda ya kai kimanin kowane mintoci 19 rayuka da yawa suna salwanta babu ceto. Ba za’a iya hana bal’I faruwa ba amma mutanen Allah zasu iya hanawa ta wurin ribato rayukan zuwa ga bege.

## DAMA

Mun riga mun hada hanu da kungiyan Mishanari wanda za’a juya wannan littafin a buga a kuma rarraba a yaruruwa 40. muhimmancin aikin Allah ya shafemu ya zama tilas, muna bukatan taimakonka.

## KALUBALE

Idan wannan littafin ya tabi rayuwan ka/ki, ko Allah ya albarkace ka/kit a wurin ceton kaunatattunsa, ko kana da nufin aika da taimako na kudi domin bugun littafin don a rarraba wa wasu.

**Bukatan Littafin kuma**...

Muna rarraba littafin kyauta ne idan kana so don Ikklisiyar ku ko kungiyar addu’arku, ko kuna bukata ku fara addu’a don batattu ko kuna bukata ku yi bita akan ribataswa,

muna rokon ku ku tuntubi:

Lee E. Thomas

P.O. Box 1058

Westlake, LA 70669

United States

Email: lthomas@pelministries.org